ko kafin aminatu ta ƙarasa ayyukan tuni aunty maimuna ta shirya al'hussain daddynsa ma ya shirya,

A gaggauce ta bawa yaron kari kasancewar ya makara school ta zubawa babansa a lunch box shima zai wuce kasuwa dan amafi yawan lokuata da abin kari yake tafiya,

Sai da ta rakasu kafin tadawo a falo taga aminatu azaune tasake gyara fuskarta,

A fakaice aunty maimuna ta kalleta kafin taɗan taɓe baki,

"aminatu yau ba school ne"

"Eh wllhy aunty banida lectures yau"

"ok kice tare zamuje asibiti kenan"

shiru aminatun taɗanyi kafin tace,

"a'a ni sai anjima zanje aunty"

"ok shikenan bara muje part ɗin hajiya daga can nizan wuce asibitin kasancewar tau da wuri zanje saboda zayyad da ya kwana acan kuma kinga saina kai masa abinci zai karya"

tsilim taga aminatu ta miƙe tareda cew,

"aunty to muje asibitin tare mana"

"A'a yanzufa na tambayeki aminatu, kuma kukacemin bazakijeba,"

Sosa kai aminatu ta ɗanyi tareda cewa,

"wllhy aunty yanzu kawai naji inason tafiyar"

Ɗan taɓe baki aunty maimuna tayi kafin tace,

"kyadaia ji da iyayinki"

A ranta kuwa tana saƙe2 a bubuwa da dama akan aminatu,

A haka dai ta ɗauki basket ɗin sukayi ɓangaren hajiya,

Koda suka ƙarasa tuni hajiya itama ta shirya suna zaune a falo ita da ummy dakuma fateema,

Da sallama suka shiga aunty maimuna ta duƙa ta gaida hajiya,kafin tazauna kan kujera kusada aminatun,

Tunda syka shigo aminatu ke zuba idanu neman khadija amma shiru hakan yasata tunanin kodai khadijan na ɗakin tane,

a ranta tace,

"Munafuka yanzun haka tana ɗaki tanayiwa wanda bai damu da itaba kwalliya"

Wani kishi ne yasake tasomata tunowwa datayi cewar tabbas ko ita tasan khadijar ta fita kyau26

muryar hajiya taji tanacewa,

"to ai sai ku taso mutafi saboda mu dawo da wuri ko"

A sanyaye ta taso itafa gsky bata so atafi abar lhadija agidan saboda bataso ace yau ma zasu tafi ita da zayyad ɗin kamar jiya,

"hajiya wai ina khadija ko bazatajeba"

"a'i Tun ɗazu khadija ta tafi makaranta sai antaso zata biya"

Saurin washe baki tayi tareda yin gaba da azamar ta,

Da idanu hajiya tabita kafin ta taɓe baki itama tayi gaba,

A motar yaya munir zasu tafi dan haka suka nufi motar yaya munir ɗin,

Ko ƙarasawa basuyiba yaya munir shima yafito daga part ɗinsu shida yaya al'ameen,

har gaban hajiya suka ƙaraso kafin yaya al'ameen yace,

"hajiya har kun fito kenan"

"wllhy kuwa aminu mutanen jigawa tafiyar ce ko?"

"Wllhy kuwa hajiya gashi zamu hau hanya"

yaya al'ameen yafaɗa tareda kamo hannun hajiya,

Itama dafa kansa tayi tana cewa,

"Allah ubangiji yatsare yakuna bada sa'ar abinda akaje nema ayi ta haƙuri da rayuwa kaji aminu"

Mur'mushi yaya al'ammen yayi tareda cewa,

"insha allahu hajjajunmu"

Ya saki hannunta yayi gaba yana ɗaga musu hannu,

Suma mota suka shiga sukayi asibitin,

A ɓan garen su merry kuwa sai da suka gama masha'arsu kafin alhajin yatafi,

Sai da yatafi suka zauna kafin fareeda ta kalli merry,

"ƙawata ya ya dai naji wayarki shiru,kinsan fa ina cikin wani hali gashi inata kiran zayyad amma yaƙi ɗaga wayata"

"nifa ina tsoron ace zayyad yaƙi yadda da abinda nakeda buƙata"

Da yaƙe a fuskar merry ta kalli fareeda,

"hmmm ƙawata kenan nidai soyayyar ki da zayyad na bani mamaki, gsky dole mu kama zayyad ahannunmu"

"wllhy ƙawata al'amuran zayyad na bani mamaki,tunda nake da zayyad fa sex bai taɓa haɗani dashiba,"

"hmmm fareeda kenan ki kwantar da hankalinki kisaka aranki zayyad nakine ke kaɗai ƙawata"

A ran merry kuwa ashar take ɗirkawa fareedar dakuma mugun al'kaba'i,

Miƙewa fareeda tayi tafara juyi agaban merry,

"ƙawata kalleni fa shin wai me narasa a duniya da yasa sai na nemi alfarmar zayyad ya aureni"

zama tasakeyi agaban merry,

Ban taɓa tunanin cewar ni fareeda akwai ranar da zan so wani namiji da zummar aure ba sannan kuma ba taaɓa tunanin zan ringa bin namiji yana wulaƙantani ba"

"Yanzu dai ba wannan ba meye mafita"

A zuciyar merry tace anzo gurin,

"shiryawa zakiyi zuwa gobe muje asibiti mu sake nemansa da buƙatar mu"

ba tareda wani dogon tunani ba fareeda tayiwa merry godiya,

Daga nan suka canza akalar hirar da yawanci surutan fareeda duk akan soyayyar zayyad ɗinne

Koda suka je asibitin yau jikin ammi da sauƙi sosai ana tunaninma in basu sallameta zuwa anjima ba to idan allah yakaimu gobe zasu iya sallamarta da wuri ma kuwa,

Dan tunda sukaje aka barsu suka shiga gurinta sunata hirarsu da ammi,

A hankali ya turo ƙofar yashigo da sallama,

Ga baki ɗaya suka haɗa baki gurin amsa masa sallamarsa,

Shi kansa yarasa dalili tunda yashigo yake baza idanunsa kamar wanda yake neman wani abu,

cikin sauri ya kawadda idanunsa zuwa duba magungunan da suke kan ɗan ƙaramin table ɗin gabana gadon,

Hnnunsa yakai kan hannun ammin yaɗagoshi tareda ɗan dubawa,

Kallonta yayi da ɗan murmushi kafin yace,

"lallai ammina ansamu lafiya"

itama murmushin tayi kafin tace"

"sosai ma kuwa rabin raina,jikina kam masha allahu ga kuma ƙwarin gwiwar albishir ɗin sirika ta data zo dubani,kaga kuwa ai dole in zanzare in miƙe tunda mu ma bana za'a dainayimana gori"

Ammi ta faɗa da ɓurmushi tana satar kallon umma,

Aikuwa an taɓowa hajiya inda yakeyimata ƙai'ƙayi,

"wllhy kuwa kedan bakiga sirikar takiba da sai kinma fi haka murmurewa,gata saliha irin wacce kikeyiwa ɗanki fata"

"Aikuwa hajiya kinada babbar kyauta mai tsoakatunda kekika fara yaba sirikata"

Dukansu dariya sukayi banda aminatu datakejin kamar an aikomata da saƙon mutuwa,

Gabaki ɗaya zuciyarta ta dawo mata maƙoshi ta wani tokareta ko miyau ta kasa haɗiyawa,

"uhmmm allah dai yazaɓa mafi alkairi dan ba'a ganewa a hijabinnanfa hajiya"

Cewar aunty maimuna,

Umma ce tace,

"kashh maimuna dama baki faɗaba ai su idanunsu a rufe yaje yanzu zaau fara ƙidayaki a layin yɗan baƙin ciki"

"ai wllhy nasani dama keda maimuna tunda kukaga yarinyar nan a idanunku naga batayimuku ba to ai saiku zaɓo masa wata tunda ku kowwa ma baiyimukuba"

"haka fa kwanaki yarinya taringa zarya tanason zaidu tsakaninta da allah amma ke maimuna ke kika tsage kikace wai ba ajinshi bace"

Hjjaju ce take wannan maganganun,

Cikin raha itama aunty maimunan tace,

"wllhy hajiya ni idannayiwa zayyad zaɓe sai yaji duk duniya ba wanda yakauni iya zaɓe"

Gabaki ɗayansu dariya sukayi,

Har shi uban gayyar saida ya ɗan murmusa tareda girgiza ka,gsky aunty maimuna ba damace,

Fuuuuuu aminatu tayi waje kamar wata macijiya,

Baki asake hajiya ta bita har ta ƙule wa ganinta kafin tajuyo tanacewa,

"wai ni kwana biyunnan ina lura da amina wani lokacin kamar mai iska,"

"sai tana walwala kuma sai kaga gabaki ɗaya ranta ya ɓaci,yarinya sai kace wadda akewa girka"

aunty maimuna ce ta tace,

"hajiya kindai san halin amnatu da zurfin ciki,amma bari in mun koma gida zan lallaɓata naji abinda yake damunta,"

dr zayyad ne ya kalli aunty maimuna yaɗan shagwaɓe fuska kafin yace,

"yanzu dan allah aunty tun safe nakiraki nace kitahon da abin kari amma tunda kikazo kiketa zuba hira kinkasa bani koɗan shayima, saboda kawai ammina bata da lafy"

Yayarasa maganarsa yana kallon ammi,

"hmmm zaidu kenan inbanda abinka yo dama kullum itace zata dawwama ci dakai,ai duk rintsi wata rana sai naga fuskar wannan kilbabbiyar matar taka wadda ƙilama mummunace"

har yafara tafiya zai fita daga ɗakin ya juyo jin maganar hajiya ta ƙarshe,

"me kikeci na baka na zuba ai matata ma sai kingaji da ganinta,sannan wai nidakaina nacemiki ga wadda zan aura,dan haka karki ƙara haɗani da kowacce mace kina zaune zan kawomiki kyakkyawar matata"

Yana gama faɗar hakan ya juya yayi gaba abinsa,

"ba shakka zaidu! kayi baki. aikuwa wllhy tunda ni ka watsawa ƙasa a ido zaka sakw samun wadda zata ringa kareka a maganar aure amma badai niba kuma wllhy ubanka zai dawo sauna turashi ya sakaka fiddo matar aure"

Shi dai dr zayyad baimasan abinda take cewa ba yayi gaba abinsa,

Sai su ammi dasuke faman yimata dariya,

ƙofar ɗakin yaci karo da aminatu tana zaune tasha uban kukan ta,shidai ya ganta amma bai wani tabbatar da yanatinta ba ya wuce warsa abinsa,

bai jima da fitaba aunty maimuna ta fito da flaks ɗin abinci a hannunta,

I tama a bakin ƙofa ta ataradda aminatun tayi uban tagumi ita ɗaya,

Bata wani nuna mata tasan tana cikin damuwa ba saima cewa datayi,

"A'a mennata eai nan kika dawo ne"

A hankali ta ɗago kanta ta kalli aunty maimuna,

Duk wanda ya kalli idanun aminatu zai tabbatar tasha kuka,

"subahanallahi aminatu kuka kuma lfy"

Wani sabon hawayenne yasake sakkowa aminatu wanda ta kasa control ɗinsa yafara zuba daga cikin idanunta,

sauke abin hannunta auty maimuna tayi tareda duƙawa ta dafa cinyoyin aminatun,

"Ameenatu lafy da kuka haka kodai wani abun yana damunkine wanda kike ganin kukan yafi yimiki daɗi akan kifaɗa mana"

Haƙiƙa mama babba ta dasawa zucoyar aminatu tsanar mutane dayawa ciki huwa harda aunty maimuna,

sai dai kima ta koyamata mugun makirci da munafurci tayadda bazaka taɓa fahimtar gskyrta ba,

Amma innnna!

Tuni aunty maimuna batun yau ba ta fahimci aminatu na son zayyad saboda aunty maimuna irin mutanennan ne masu baiwar fahimta,

A hankali aminatu tasaka hannunta tashare fuskarta kafin takalli aunty maimuana ta ɗanyi yaƙe tace,

"wllhy aunty haka kawai nakejin raina yaɓaci sai luma wani ciwon kai danakeji"

duk da aunty maimuna tasan kome yake damun amimatun kuma tasan duniyanci tayimata na ɓoye mata damuwarta yasa tace,

"habbba aminatu meye abin kuka saboda ciwon kai keda kikeda yaya dr,uym ki kwanyar da hankalimki yanzu muje office ɗin yayanku sai yabaki ɓaganin kinji ta wajena"

Aunty maimuna tafaɗa tareda miƙar da ita tsaye ta ɗauki flask ɗin suka nufi office ɗin,

da sallama aunty maimuna suka shiga office ɗin dr zayyad,

Yana waya hakan yasa shi ɗaga musu hannu,

"ni ban wulaƴanta kiba kedai kike ganin hakan,inada baƙi ina zuwa"

Ɗib,ya kashe layin farreda dasuka kirashi itada merry,

Da ɗan murmushi ya kalli aunty maimuna tareda buɗe flask ɗin gabansa,

Sosai ƙamshin abincin ya daki gancinsa,

Ai kuwa ya wani lumshe idanunsa tareda shaƙar numfashinsa,

Cikin raha aunty maimuna tace,

"ba'a saba cin irin wannan ba ko?"

Shima murmushi yaɗanyi kafin yace,

"amma aikinsan bai kai na ammi ba ko"

Ɗan kallon sama tayi kafin tace,

"uymmmmm!amma dai kasan nafi amaryar da zaka aura ko"

Kallon sarious yayi mata kafin yace,

"wai ni aunty kinwani damu kanki kwanannan da maganar aurena ahin koko dai kinsamomin matar da zan aurane"

"In kabani dama zayyad kadaisan bnafika iya zaɓi tunda nazabo daddynka ko?"

"Kayyyy aunty abin harda zagi"

"ba zagi zayyad gsky nafaɗa"

"to nabaki aunty amma kisani infa batayiminba zance batayiminba"

"albishirinka"

"goro"

"fari ko ja"

"Fari tass auntyna"

"OK to meye goron albishir ɗin"

"me kike so"

"matar da zan samo maka ba itace zatace tanasonka ba kaine da kanka zaka faɗa tarkon ƙaunarta sannan kuma kace kanasonta, inhar hakan ta kasance zakabani kyautar sabuwar mota"

Dariya yayi sosai kafin yace,

"gsky aunty kin ɗaukeni yaro! karkimanta fa na girmeki amma zakiyimin wayo"

Kallonsa tayi ido cikin ido kafin taci sarious tafara magana da tsantsar gsky,

"Zayyad nasan ka girmeni amma a haka zaka faɗa tarkon zaɓin daznyimaka sannan kuma kai da kanka zayyad mai taƙama da gayu zaka zama bawan wadda na zaɓa maka inkuma haka takasance kayadda zaka bani mota sabiwa dal"

shima cikin sarious ya kalleta kafin yace,

"ni zayyad na yadda in har na faɗa ƙaramin tarko irinnaki zan baki kyautar sabuwar mota da naira dubu ɗari biyar cash"

Cikin tsabar murna da ɗoki ta kama hancinta kafin tace,

"wllhy badan muna asibitiba da sainayi guɗa da wannan al'ƙawarin da ka ɗauka"

Yiffffffff,sulaji faɗuwar aminatu tsabar sanyin da ƙafafunta sukayi,

Da sauri aunty maimuna ta yi kanta dan ita har ga allah tama manta da maganar aminatun,

kamo hannunta tayi ta taimakamata tamiƙe tsaye tarda zaunar da ita gaban kujerar zayyad,

"kaga kasama na shagala da amunatu,wai kantane yake ciwo shine nace tazo muje kabata magani"

Zayyad kuwa dayake jikin kujera kallon aminatun yayi kafin a hankali ya taɓe bakinsa da cewa,

"ta sha paracetamol zai daina,ai shegen yawon tsiyane dasu,"

"in kunkoma aunty kice su umma su haɗa kayansu da ƙarfe biyu zaau tafi gida"

" Yawwa alhamdulillah"

A ɓangaren su merry kuwa tun ƙarfe goma merry tazo gidansu farreda wai dan ta ƙara yadda ta damu da ita da matsalarta,

Meeryn ce ma tasaka fareeda ta sake nacewa kiran zayyad ɗin har ya ɗaga sun ffara waya su aunty maimuna suka ahigo wanda hakan yasa ya kashe wayar gabaki ɗaya ma,

Sosai hakan yatadawa farreda hankali wanda merry ta turata wai ta shirya suje aaibitin,

haka kuwa akayi a take farreda ta tashi ta ahiga wanka,

Tana ahiga merry ta buɗe wadrobe ɗinta ta zaɓo mata wasu matsiyatan fitinannun kaya,

koda fareeda ta fito tasoyin ƙorafi akan kayanda merry ta zaɓo mata amma merryn taƙi bata dama,

Kasancewar itama merryn danata wayon akan fareeda tasaka wannan shigar banzar,

Tunda tasan oyayen zayyad suna nandan haka dole zasu ga fareedar kuma hakan zaisaka su takurawa zayyad akan sai yayi aure,

To daga nan ita kuma sai taci gaba da ahigemusu a mtsayin saliha kuma mai son ɗansu har tasamu damar aureshi,28&29

khadija kuwa sai ƙarfe biyu suka tashi dafa school ganin ana ƙwala rana yasata nufi gida da nufin idan ta sake shiri saita nufi aaibitin,

A gajiya take sosai koda taje gida ba kowwa a gidan sai su mama babba dasuke part ɗinsu da umma ƙarama,

Hakan yasa direct tanufi part ɗin hajjaju ta,

kanta ne yakeyimata wani irin ciwo hakan yasa tanayin wanka ta sha magani tafaɗa kan gado da nufin taɗan huta sai ta nufi aaibitin,

Aikuwa tana kwanciya bacci yayi awon gaba da ita.

Sai ƙarfe ukku da minti goma ta farka ganin lokacin da agogo ya nuna yasata miƙe cikin sauri tafara shirin zuwa asibitin.

Ba wani ɓata lokaci ta turare jikinta da turaren wutar ta kafin saka wando da riga na pakistan baƙi da adon golden,

Ba wani kwalliya ta tsaya yiwa fuskartaba iya powder da lipstick kawai tasaka sai ta ahafe jikinta da turaren gold amber gabaki ɗaya ƙamahin jikinta ya rikiɗe yabada wani ni'imtaccen ƙamshi na musamman,

Ganin yanayin ahigarta yasa ta dakki wani aah ɗin hijabi mai kyau kalar na zamani tasaka dogone har ƙasa,

Gsky khadija nada kyau na ban mamaki dankuwa ɗas ta fito acikin hijabin kamar zaka saceta ka gudu.

A can asbiti kuwa koda aunty maimuna ta kama hannun aminatu suka nufi komawa ɗakin da ammi take.

Gabaki ɗaya aminatu batasan inda take ɗora ƙafarta ba jinta take kamar ba itaba.

Babu abinda takeji sai maganganun su aunty maimuna da yaya zayyad wanda takejinsu kamar zasu fasa mata kunnuwa.

Itafa tama rasa me zata tunana.

shin wai me suke nufine,anya kuwa zuciyarta nayimata adalci akan soyayyar zayyad kuwa,

A gsky bazata taɓa iya jurewa ganin zayyad inuwa ɗaya da wata ba itaba taɗaukarwa ranta alwashin ganin bayan dukkan wanda yake burin rabata da soyayyar zayyad ko waye.

A haka batasan sun iso ɗakin da aka ajiye amminba,

saida aunty maimuna ta ɗan taɓota kafin tayi wata iriyar firgita.

Hannunta aunty maimuna taɗan murza da ƙarfi kafin ta daidaita amma daka kalleta zakasan tana cikin damuwa,

Hajiya ce ta kalleta cikin sigar lallashi tace,

"wai ni kam amina meyake damunkine naga duk kin canza kamar wadda batada lakka ajiki,ga wata faɗawa dakikayi"

a yanzu dai duk iya duniyaci na aminatu ta kasa koda yaƙenma sai raba idanu datake famanyi a tsaye,

Gudub karta sake faɗuwa yasa aunty maimuna nuna mata kujera da idanu.

Aikuwa kamar me jiran umarni ta zauna akan kujerar kamar saƙago,

Aunty maimunace takalli hajiya tace,

"wai kantane yake ciwo shinefa duk tashiga damuwa"

Ba tareda tabawa hajiyar wata dama ta yin maganaba tacigaba dacewa,

"uhmmm hajiya kingafa har zanshiga zance na manta zayyad yace mu haɗa kaya za'a sallamemu"

Hajiya da umma ne suka haɗa baki gurin cewa,

"Masha allahu"

cikin raha aunty maimuna taɗan kalli ammi datake lazimi tace,

"a'a fa hajiya kubar murna naga kamar har yanzu jikin ammi bai ƙarasa watssakewaba"

Aikuwa da sauri ammi ta ɗago idanunta tana murmushi ta kalli aunty maimuna tace,

"hmmm haba aunty ai wllhy ninasan nafiki lafiya"

"Kayyy ammi anya kuwa to kuma ai naga babu alamun hakan a jikinki"

A jiye carbin hannunta ammi tayi tareda yin bissimillah ta sauko daga kan gadon datake ta kalli aunty maimuna da murmushi,

"na sauko ƙanwata mezanyimiki a tabbatar nasamu lafiya"

"hmmm ammi anya kuwa"

"kina tan tamane"

"To goyo"

Aunty maimuna tafaɗa da yar dariya,

Gabaki ɗayansu dariyar suka yi kafin mama ta tashi tafara haɗa kayansu,

ana hakan dr zayyad ya shigo ɗakin da sallama a bakinsa daga ganinsa daga masallacin asibitin yake,

Ganin ammi a tsaye yasashi komawa daga gefenta a tsaya tareda kama hannuwanta ya ɗaura kansa a kafaɗarta,

"ammina ya naganki a tsaye"

Zayyad ya faɗa da husky voice ɗinsa,

"hmmmm to yarona ai jiki yayi kyau kaga gwamma in ringa ƙarfafawa ko?"

"kumafa hakane gaskiya"

Ya faɗa yana kallon ammin,kafin yajuya kallonsa ga aunty maimuna,

"auntyna maigidanki fa zaki kirawo yazo yatafi daku saboda gsky inada ooeration banda ƙarfe ukku da rabi dan haka bazan samu damar komawa gidaba sai zuwa dare"

"Ok ba matsala bara nakirashi sai yazo mutafi"

ammi ce ta kalli aunty maimuna tace,

"a'a gsky ba sai ankirashi ankatse masa kasuwarsa,sai dai ko akira ahmad ina ƙila yadawo daga school sai kabashi motarka yakaimu imyaso sai yadawo maka da ita shikuma ya hau abin hawa yakoma gida"

Tunda ammi tafara magana hajiya ke sakamata albarka da yaba baiwar hankali irinna ammi dama sauran pan uwanta sirikkan hajiyar,

"yadda kikace haka za'ayi ammina"

DR zayyad ya faɗa yana ɗaga wayarsa dankiran ahmad,

bugu biyu wayar tayi ahmad yaɗauka cikin girmamawa,

"Assalami alaikum"

"wa'alaykassalam"

"Yaya ya aiki"

"Maaha Allah,inason ganinka asibiti yanzu"

"OK badamuwa insh.... "

ko ƙaraswa baiyiba zayyad yakashe wayarsa gamida maidata cikin aljihunsa,

Yasake kallon su hajiya yace,

"bara na je office yanzu za'a kawo muku takardar sallama"

Bai tsaya jin me suke faɗaba yayi gaba abinsa ya nufi office ɗinsa,

"hmmmmmm"

Aminatu ta saki wata nannauyar ajiyar zuciya wadda tasasu gabaki ɗaya kallonta,

Ita har ga allah bama tasan me yake faruwaba,

Tunda zayyad ya tsaya idanunta suka tsaya akansa zuciyarta na yɜara azalzakarta da soyayyar zayyad ɗin. A ranta take cewa,

"gsky yaya zayyad duniyane ta tabbatar babu macen da zata iya ɗora idanunta akan yaya zayyad ɗin batareda ta saukesu da cikakkuyar ƙaunarsa ba,

Sheɗaniyar zuciyarta tacigaba da hankaɗa ta akan ra'ayinta na tabbatarwa kanta dole ne ta mallaki zayyad kota halin ƙaƙ"

ammi ce ta ɗan matso jikinta tareda dafa ta tace,

"Sannu kinji ɗiyata"

firgigit ta yi saurin ɗaga idanu suka haɗa ido da ammi,

"sannu ɗiayata kinji bari muje gida sai ki samu ki ɗab kwanta lozakusamu reliep"

Yaƙe taɗanyi kafin a ranta ta fara tsinewa ammi saboda a ganinta ammin katangace dake tsakaninta da zayyad.

A gsky ba namijiba ko mace ta kalli irin shigar da fareeda tayi sai taji wani tanayi ajikinta,

irin shigarda tabbas idan ke uwar kirkice kika kalli fareeda saikinyi gaggawar nema mata shiriya daga Allah,

Riga da wando tasaka wayanda sukayi matuyar karɓar jikinta sunti masifar yimata kyau rigar ƙaramace sosai wadda muddin zatayi kyakkyawan motsi sai ka hango cibiyarta,

Sai wani arnan wando data saka wanda yafitar da gabaki ɗaya sharp ɗinjikinta sosai ya ɗameta sai wata top mai dogon hannu wadda taji duwatsu mai kyau sosai wadda batada maraba da rariya,

Takalmi tasaka high hill mai shegen kyau wanda yaji duwatsu a samansa,

Sai kuma jakarta ƙarama datasaka wadda tayu daidai da tsarin sgigarta dakuma takalminta,

Sosai ɗaurin ɗankwalinta ya zauna daram akanta gakuma wivon na atach data saka,

Gsky ba ƙarya fareeda tayi kyau sosai ga wani sihirtaccen yamshi datake bazawa nai ɗaukar hankali,

A yangance tafara juyi tana nunawa ƙawarta merry tsarin,

A gsky da ace zaka buɗe zucoyar merry to da zaka tabbatar da itama ba baya bace a fagen danƙararriyar ƙaunar zayyad ɗin saboda yadda wani baƙinciki ya narke acikin zuciyarta da azababben kishin dayake taso mata,

Wai yanzu tana gani farreda zata tafi gurin mijinda zata aura kuma mallakin zuciyarta da wannan shigar,

gsky da badan plain ɗinta akan fareedar ba babu abinda zai hanata wulaƙanta fareedar dakuma nuna mata iyakar ta akan zayyad ɗin,

Sai dai kuma akwai lokacin da sai tasaka fareeda hawaye da idanunta wannan alwashine sai ta nunawa fareeda ceewar zayyad ba kalarta bane,

Lokaci na zuwa da fareeda zatayi nadamar saninta sannan kuma zata tabbatar mata itafa cikakkiyar yar barikice,

"gsky yawata dolene yau ɗinnan zayyad yashiga tarkinmu.irin wannan ado haka dole mu nuna wa zayyad mufa ba ƙasgin yar wa bane,

Sosai farreda taji daɗin yabon da merry tayimata ta wani washe baki tare da yin farrr da idanu,

A fa kaice merry ta bankamata wata muguwar harara kafin ta wayance da yin murmushin yaƙe,

"wannan farin a ajiyewa zayyad dan na tabbatar zai masa amfani"

Bata bata damar yin maganaba ta diba agogo tareda yin saurin cewa,

"gsky yakamata mutafi kingafa har ƙarfe ukku da rabi"

"ok ba matsala mutafi"

Itama merry ɓiƙewa tayi suka nufi hanyar fita,

A asibitin kuwa tuni sun gama haɗa kayansu har ahmad ma yazo yafara fita da kayan yanasaka su mota,

Sai da ahmad ya kammala tsaf kafin suka fito daga ɗakin,

A cikin corridoor ɗin ɗakin suka haɗu da zayyad yati shirinsa cikin kayan da zai shiga aikin,

Sosai kayan sun amshi tsarin jikin zayyad ɗin da farin glas ɗim dayake maƙale da idanunsa,

"masha allah"

duka suka faɗa amma muryar ammi tafi ta kowwa fita dayake tafaɗane da ɗan sauti tana murmushi ta kamosa jikinta,

"Allah yayimaka albarka da ƙannenka gabaki ɗaya ɗana,"

Mirmushi yayi yace,

"ammi na sai gida ko?"

"to ɗana tunda jiki ya warware ai zaman asibiti ba daɗi damma dakai"

Murmushin jin daɗi ya fitar me sauti,

hajjaju ce taja ƙafarta gaba tana mita,

Wanda hakan yasasu yim ƙaramar dariya,

A hankali suke tafiya sai da zayyad yaraka ammi har bakin mota yaga ahigarta da tafiyarsu kafin ya koma cikin aaibitin,

A daidai bakin gate zasu fita su kuma su farreda motarsu zatashigo,

To dayake aunty maimuna na ta jikin windoe kuma window ɗin abuɗe ne yasa sukayi ido biyu da merry da take driving,

Dayake suma nasu glass fin a ɗan sake yake,

Ai kuwa sosai gaban merry ya faɗi ganin sunyiwa juna kallon ido cikin ido da matarda ta tsaya acikin zuciyarta daram,

Tsabbb aunty maimuba ta ganeta tareda yimata kallon na fahimceki kuma na raina naki wayau,

Da sauri merry ta janye idanunta tareda yin azamar duƙar da kanta,

Tuni motarsu aunty maimuna ta wuce hakan yasa fareeda bata wani san meyake faruwa ba

30&31

Duk da aunty maimuna ta sake fahimtar abubuwa da dama a ɗan kallon dayashiga tsakaninta da merry hakan baiwani sa ta nuna damuwa a fuskarta ba,

A hankali merry ta parking motar a inda aka tanada dan ajiye motocin,

Sun ɗauki mintina acikin motar suna tattauna yadda fareeda zata jawo hankalin zayyad,

Amma agefe guda merry nayiwa fareeda shune ne ta hanyar da dole sai ahalin zayyad ɗin sunganta duk da kuwa bataso ganin fitar aunty maimunan ba taso ace sun haɗu da fareeda,

Amma kobasu haɗu yanzuba tasan dole fareeda zata hadu da yan uwan zayyad sannan kuma a yanayin shigar da ta tura fareedar tayi tasan duk wani mai mai mutunci bazai so ace fareeda ta kasance daga ahalinsa ba,

"fareeda wannan wata babbar damace da zamuyi amfani da ita dan haka kisan duk hanyar dazakibi dan ki tabbatar kinja ra'ayin zayyad akan abinda mukeda buƙata,karkiwani damu da cewar nan asibiti ne inason ki fara jan hankalin ɗaukacin mutanen asibitin yazamana kowwa yasan ke wacece kuma suga gurin eanda kikazo,hakan shine zai bamu damar cimma burikanmu"

"gsky ina aldahari dake ƙawata bazan taɓa baki kunya ina mai tabbatar miki saikin ganmu a inuwa ɗaya nida dr nah"

Wani malalacon kallo merry tayiwa fareeda wanda saika cika cikakken ɗan bariki zaka iya fahimtar inda kallon yadosa,

A hankali farreda ta buɗe murfin motar tareda sakko ƙafarta ta fito,

Ta ɗauku yan sakanni tana ƙarewa asibitin kallo kafin tafara taku cikin wani salo na musamman da ba kowwa ne zai iya kallonta sau ɗaya ya ɗauke kansa ba,

Yanayin yadda take karya jikinta dole mai ƙaramar shawa zai tsaya kallonta da ƙoƙarin damƙe hajiyarsa dan sosai take juya madaidaitan mazaunanta dasuka ɗame cikin fitinannen wandon datda saka,

Wata zazzafar ajiyar zuciya merry ta sauke tareda kwantar da kujerar ta tabi jikinta,

"lallai farreda bakida wayau naki wasane"

A haka fareeda ta osa har ɓangaren da office ɗin zayyad ɗin yake,

Batareda ta damu da yanayin kallon da mitanen gurin suke binta dashiba ta tsaya bakin office ɗin tarda yin nocking sai wani yauƙi take da sigar cikakkiyar yar bariki,

Dr zayyad kuwa dayake tsaye bakin ƙofa kuma a shirye tsaf da kayan aiki yabuɗe ƙofar tareda zuba idanunsa akan fareedar da bai tsammaci ganintaba,

dirar mikiya idanunsa suka saukar masa da ganinsa kan fareedar da ta tabbatar yanayin shigarta tabbas dole ya rikita gwarzonnata,

Aikuwa cak idanunsa suka tsayar dashi akan surar jikinnata da yake bi da wani kayataccen kallo,

ganin hakan yasa itama farredar ta fara neman canza salonsa da kashemasa idanu tareda lasar lips ɗinta,

Ko motsi dr zayyad baiyiba kuma har yanzu idanunsa na kanta da zazzafan kallonsa da ta tabbatar da zai iya juyewa ako da yaushe,

A hankali ta ranƙwafo ƙirjinta batareda ta ɗaga ƙafafaunta ba ta yo duƙo da niyyar hura masa iska a idanunsa,

Tana sane ta manna illahirin nonuwanta a jikin ƙirjinsa tareda hura masa sassanyar isakar bakinta datake tafe da ƙamshin sinadarin saka ƙamshin baki,

aikuwa ya wani lumshe idanunsa a cikin wani irin slow,

Ganin hakan yasa tasake goga masa ƙirjinta cikin wani salo dayasakashi sauke wani malalacin nishi da bai shiryawa zuwansaba,

Tunda ta fito daga gidan take ɗan sauri sauri dan ganin har ƙarfe ukku da arba'in a daidai bakin layinsu tasamu abin hawa ta tsayar tareda cemasa,

"Aminu kano"

ta shiga yaja suka kama hanyar asibitin,

kwata kwata bata ma kawo cewar ansallami ammi ba kasancewar babu waya a hannunta bare kuma wani yakirata ya faɗamata,

Hakan yasa batama wani lura da motarsu ammin ba lokacinda suka hau babban titin asibiti lokacin sukuama motarsu zata sauka zuwa layom dazai sadasu da gida,

Kodavsukaje asibitin ta sauka kafin ta biya mai adaidaita kuɗinsa,

A hamkali cikin nitsuwa ta nufi cikin katafaren asibitin,

Direct ɓangaren da aka kwantar da ammi can tanufa watakam emergency,

Koda ta shigo cikin harabar ɗakin da aka kwantar da ammi amma bataga kowwa ba hakan yasa direct ta nufi ɗakin da tasan ammin take a tunaninta ko suna ciki,

A hankali ta tura ƙofar ɗakin kasancewar ba wani daɗewa sukayi da fita ba yasa ba'a rufw ɗakinba,

Ganin datayi wayam ɗakin babu kowwa yasata tsayawa ta fara tunanin to ina suka nufa,

Kodai ansallamesune?,

To kuma inda ansallamesu aida sai wani yakirata ya faɗamata hakan,

To inama wayar da za'a kiratan bayan wancan mugun ya cillar mata da waya saboda tsabar zalinci da mugunta,

A sarari ta furta,

"Allah ya isa wllhy mugu kawai"

Kome ta tuna kuma!oho tadaiti saurin saka hannunta ta rufe bakinta tareda ɗan yin waige waige kafin ta ɗan ɗaure fiska tareda yin gungunin da na tabbatar ba alkairi ta faɗa ba,

"to kodai ciwon ammi ne ya tashi aka canzamata ɗaki"

Wata zuciyar ta faɗa mata,wanda hakan yasa zuciyarta bugawa da ƙarfi,

da sauri ta juya a guje ta fito daga ɗakin wanda hakan yayi daidai da shigowqar wani saurayi ɓangaren,

bata wani damu da sanin ko waye ba tayi gurinsa tareda tambayarsa acokin tashin hankali,

"dan allah ko kasan meyake fariwa da matar da aka kwantar a wannan room ɗin,"

"shima da ɗan tashin hankalin yadda yaga ta wani birkice ya fara magana,

"eh to gaskiya banida wata masaniya da hakan amma dai ɗazu naga wasu daga nan room ɗin sun nufi office ɗin DR zayyad,sai dai nasan patiete in ansallameshi ai bazai nufi office ɗin dr ba,amma ki ɣarasa office ɗin inada tabbacin zaki samu cikakken bayani acan ɗain,"

Ita har ga allah tama mance da wani hukunci data ɗauka na yanke duk wata alaƙa da abimda zai haɗa ta da yaya zayyad ɗin kamar yadda ta faɗa, dan kuwa ko kafin saurayin yaƙarasa faɗar abinda zai faɗa tayi office ɗin yaya zayyad ɗin aguje,

ɓangaren su zayyad kuwa jin nishin dayake sali yasa farreda taƙi bashi damar ko matsawa daga yadda suke saima sake matsemasa da tayi tareda saka ɗan yatsanta ta fara zagaya kyakkyawan sajensa dayayima fuskarsa wani masifaffen kyau,

Tuni ta fara canza salon dr zayyad ɗin da yanayin nata salon idanunsa har sunfara camza da maitarsa ta sh'awa datake shirin ɓallewa,

Bakinta takai saitin labbansa tareda zaro harshenta ta ɗora akan laɓɓan nasa tafara lasa,

sake lumshe shanyayyun idanunsa yayo dasuka yi masa wani irin nauyi,

Tareda ɗaukar hannunsa da ƙyar ya ɗaura akan bayanta ya ɗan sake turota jikinsa,

Aikuwa ta wani sake manna jikinsu gurin ɗaya tareda haɗe bakinsu,

Tuni suka fara bawa juna wani zazzafan kiss da sai ka rantse mayun watan zakunane,

Sosai zayyad yadage wajen shafa jikinta tareda mammatsa jikinnata zuwan kunnuwanta,

Da gudu tashigo ɗan coridor ɗin dazai sadata da office ɗinsa wanda gabaki ɗaya ma gurin babu mutane kasancewar ba gurine da mutane ke yawan zuwaba,

sai datazo dab da shiga office ɗin kafin idanunta sukayi mummunan ganin da yasakata cikin tashin hankali da nadamar zuwanta ofgice ɗin,

Da sauro ta fara ja da baya kafon ta saki wata razananniyar ƙara da saida suka dawo hayyacinsu tareda saurin saki juna suka kalli ɓangarenda khadija take gabaki ɗayansu,

Tuni hawaye sun ɓallewa idanun khadijar,

Zuciyarta ce ma ta tsaya cak takasa koda tuna mata meyake faruwa,

Gani khadijar kuwa ba ƙaramin girgiza zayyad yayiba amma dayake cikakken ɗan duniyane sai ya wani wayance da tsuramata idanunsa,

A hankali ya fara takawa zuwa inda take ganin hakan yasata fara ja da baya tana bim bango har tazo bakin office ɗinsa,

Bai bar binta hakan uasaka riƙe ƙofar da ƙarfi tareda dakewa tana zubarda hawayenta,

Sai da ya ƙaraso inda take kafin ya tsareta da idanunsa sosai yake kallon yadda hawaye ke ambaliya a fuskarta,

duk duniyanci da ƙwarewar bariki irinna zayyad yaji wani yanayi a jikinsa na babu daɗi,duk da bawai nadamar ganinsa danfarreda da khadija tayi bane yasashi jin ba daɗin danshi a ganinsa ba wani abubane tunda ba a wani hali ta iskeshi da fareedar ba,

Amma yaji ba daɗi da gani yadda yanwarsa take zubadda hawaye akan wani abu data gani daga gareshi wanda baimata daɗiba,

A hankali ya ɗaga hanninsa da niyyar kaiwa kan fuskarta ya sharemata hawayenta a karon farko da zai lallashi ɗaya daga cikin ƙannensa,

Sai dai kuma ganin abimda yake ahirin yi yasaka ɓangarorin biyu da suke a daskare saurin harzuƙowwa da niyyar ɗaukar matakai dabam daban,

A ɓangaren khadija wata ƙara ta ƙwalla tareda ƙanƙamewa guri ɗaya wanda yasa dr zayyad saurin janye hannunsa dan a tunaninsa wani abin ya faru da ita,

cikin shashhekar kuka tafara cewa,

"wllhy in kataɓani allah ya isa ai dama na daɗe da fara tunanin kai ɗan iskane ashe kuwa hakane tunda gashi har karuwai kake bi shine zaka ringa neman yimin sharri "

haka dai khadija tafara ihu da surutai da sai ka rantse bata cikin hamkalinta,

to farreda ma ganin zayyad zai kai hannunsa kan khadija yasata harzuƙowwa a fusace ta tsaya a gaban khadijar cikin ɗaga murya tafara magana,

" ke dallah sha'sha dabba kawai,baccinma hauka da rashin tunani da tsabar rashin ilimi da duhun kai kinga mutane a guri ki fara yimusu ihu aka,"

Sosai itama fareeda take ihu da hargowa tareda faɗawa khadija maganganu batareda tasan kowacece ba,

ita kanta khadija tayi mamakin yadda fareeda ta tsaya a gabanta take mata wayannan magamnaganun to saidai kuma bata ita takeyi ba,

ita fa har ga allah hankalinta ya tashi da hakin dataga ɗan uwanta aciki,

muryar fareeda ce ta sake dakar dodon kunnenta a karo na farko da ta maida hankali dajin maganar bidurwar da zucoyarta ta raɗawa suna kilaki,

"nina tsani rashin wayewa da jahilci amma yanzu abinda yake cutar mafi yawan yara kenan kwata kwata oyayensu basu....."

Ai kafin merry ta ƙarasa maganarta tuni khadija ta ahammacesu gabaki ɗayansu daga ita har zayyad ɗin,

kawai sai jin khadija yayi ta yi kan fareeda,

da sauri shima yanufesu amma innnnna!

Ko kafin ya ƙarasa tuni khadija ta rarumi ƙafafun fareeda,

Abinka da takalmi hill aikuwa tawani yarɓar da ita da ƙarfi bakinta da goshinta suka daki ƙasan tiles ɗin wajen,

Batareda wani lura da jinin da yake fita ba khadija tabita ta danne ta fara dukanta ta ko ina,

Duk da bawai khadija tafi ƙarfin fareeda bane amma tariga tayimata dabaibayin da bazata taɓa iya mirginawaba gakuma azabar da kanta yakemata na daku dayayi ya fashe,

Da ƙarfi zayyad ya finciko khadija daga jikin fareeda amma innna ta riga da ta manne ajikin fareedan sai da yayi dagaske kafin ya fincikota ta faɗo jikinsa,

Fisge fisgwn datakeyi sai ta koma jikin fareeda yasa Dr zayyad ɗaga hannunsa ya kwaɗa mata mari,

jin azaba dakuma raɗaɗin saular marin yasaka khadija wawurar hannun yaya zayyad tareda danna masa wani mahaukacin cizon dayasakashi saurin tureta daga jikinsa,

Aikuwa a fusace tasakeyin kan fareeda datake kwance jini na zuba daga goshinta da bakinta,

Shima zayyad a fusace yasakeyin kan khadijar tareda rarumota ya matseta a ƙirjinsa,

Kolowar dasukeyine yasak maɓallin rigar zayyad ɗin buɗewa wanda hakan yabayyyana shatin lafiyayyen ƙirjinsa ta inda babu best ɗin,

Aikuwa khadija ta sake daidaita tsakiyar lafiyayyun gashin dasuke baje a ƙirjinsa ta sake manna masa wani cizon tareda jan gashin ƙirjinnasa da ƙarfi,

bai san sadda yasaki ƙara ba tareda turata baya da ƙarfi ta faɗi,

ya zuwa yanzu khadija ta tabbatarda sosai ran yaya zayyad ɗin yaɓaci kuɓa muddin tabari ya damƙeta zai iya yimata lomai ma a gaban ballagazar karuwarsa dan haka a guje tamiƙe tareda banka ƙofar office ɗinsa ta ahige tareda maidawa ta rufe,

A fusace zayyad ya biyo khadijan amma ganin ta rufe yasa yakoma kan fareeda dan bata taimakon gaggawar jininda yake fita daga kanta,

Wata nurse ce tashigo kiran dr kasancewar anata jiransa amma ganin halinda fareeda take ciki yasata ruɗewa cikin sauri ta nufeta,

sosai shima ƙirjinsa ke masa azaba amma ganin nurse ɗinnan yasakashi daurewa tareda bata umarnin taimaka fareeda da tretment shi kuma ya juya yasakawa ofgice ɗinsa mukulli ya rife khadija tareda wucewa gurin yiwa patiente ɗinsa aiki,

To a ɓangaren merry kuwa tana can zaune tanata chat ɗinta abinta a zuciyarta tana ayyana irin wulaƙancin dazata ga iyayen zayyad ɗin sunyowa fareeda,

Ganin shirun ya fara yawane takumasan da ace ansamu yadda takeson da tuni yʻan uwan zayyad sunyo fatali da farreda ne yasata ɗaukar wayarta ta kira wata nmb,

Bugu biyu aka ɗaga tareda cewa,

"ranki ya daɗe"

Itama ba tareda damuwa da rashin sallama ko amsawa ba tace,

"yawwa,wai meke faruwa acikin asibitinnanne"

"kinga ɗaxu rashin katin kirane yasa ban faɗamiki ba anfa sallami yʻan uwan oga dan tun ƙarfe ukky ma suka tafi,

Cikin zafin nama ta miƙe daga kwancoyar datake a jikin kujerar mota tareda cewa cikin faɗa,

"gsky banga amfanin biyanka danake ba inbanda rainin hankalo da rashin mutunci nizaka yiwa haka,watakam ma yaudarata kakeyi kenan dama a banza nake biyankane dazaka ringa faɗamin wai bakada kati,"

Sosai take zuba riean masifa kafin cikin tashin hankali ta kashe wayar tareda neman lambar fareeda,

dolene tasan ko a wanne hali ake cikin dan kuwa zata iyayin koma meye muddin akan soyayyar zayyad ne,

Bata burin yin tozali da wani farincikin tsakanin zayyad da wata macema bare kuma fareedar,

jin ringing ɗin wayar fareedar a kusa da itane yasata sake jin wani mugun haushi,

A fusace ta ɓalle murfin motar tareda fitowwa cikin eani yanayi mai wuyar fassara,

Sai dai kuma wani tunani daya ɗarso mata a zucoya wanda uasakata saurin komawa cikin motar kamar mahaukaciya tasake rarumo wayarta tareda sake nemo lambar mutumin dasukayi waya dashi a ɗazu,

Bugu biyu wayar tayi aka ɗaga daga can ɓangaren amma saidai wanda aka kira ɗinne yana amsa wata wayar hakan yasa ta katse wayar tareda sake kiran nmbr fareedar,

Sake jin ring ɗin wayar datayi akusa da ita ne yasaka sake ƙumewa da wani mugun haushi, ko kafinkitan ya tsinke ta katseshi cikin gaggawa tareda sake maida kiran kan nmbr ɗazu,

Har yanzu dai ana amsa kura da wayar acewar batiriyar da take saita naurar kiran,

Da ƙarfi ta willar da wayar tareda ɗora kanta akan stiaring motar zuciyarta ce kemata wani irin tafarfasa,

ring ɗin da wayarta ne da taji yasakata ɗaga kanta da sauri tareda wawuro wayarta batareda ta tsaya dubawa ba ta ɗauka ko sallama babu ta fara magana,

"wai yazanta kiranka amma kaƙi ɗaga wayata iro nifa gsky nafara saka maka ayar tambaya da zargi akan lamarin ka da ba haka kakeminba,"

"yanzu dai yakamata ki ajiye duk wannan kifara faɗamin dalilin kiranki kafinnan sai kiyi faɗan hajiyata"

Daga ɗayan ɓangaren aka faɗa cikin raha kafin aka cigaba da cewa,

"batun kuma kisaka ayar tambaya akaina ko kice kinfara zargina ai bai tasoba saboda dani dake gabaki ɗayanmu babu mai gaskiya dan haka aiki nakeyimiki kinabiyana bawai iko kike daniba"

Sanin halin wanda take wayar dashine yasata sauko da murya a hankali kafin tafara magana cikin sigar lallashi,

"pls iro rainane a ɗan ɓace amma kayi haƙuri,yanzu dai dan allah inason sanin halin da ake ciki a cikin asibitin tsakanin fareeda da zayyad saboda yanzu tashiga kuma banji sakamakon danaso jiba,"

Ɗan taɓe baki yayi kafin yacemata,

"badamuwa yadda kikace"

D a sauri tace,

"yawwa iro na gode"

Kafin ta sauke wayar da wata ajiyar zuciya mai nuna tsabar rashin jin daɗin yanayi,

A ɓangaren wanda ka kirawo da iro kuwa koda merry ta kashe wayar sainaga yavigaba da magana batareda yasaukeba,

Sai dai kuma abinda yayi matuƙar bani mamaki shine,

Yanayin maganarsa zai tabbatar maka ba da merry yake magana ba saboda yana magana ne da girmamawa.....YAR MUTAN MURAYE CE GARKUWAR MITANEN DAURA ALHERI MUTANEN MASHI,

INA MIKA GAISUWA GA KAFATANIN YAN 2014 CANDY DATE MUSAMMAN MASHI DA SHARGALLE

32&33

cikin wayar da iro yakeyine aka ɗanyi wani murmushi tare ɗan jan iska kafin akace,

"ba damuwa malam iro nagode za ka iya zuwa kayi aikinka"

"badamuwa hajiya"

Ya faɗa kafin yakashe kiran tareda yin hanyar dazata sadashi da cikin asibitin,

A ɓangaren merry kuwa ana ɗaukarta aka nufi wani ɗan madaidaicin ɗaki da ita dan gyara mata ciwon dayake jikinta,

Shima zayyad ɓangaren aikinsa ya nufa,

Dan haka har aka gamawa fareeda treatment bai zo ba yana gurin aikinsa,

to itama dai fareedan bata tsaya jiransa ba dan ana gamawa ta kwaso takalmanta a hannu ta nufo hanyar fitowwa,

A daidai bakin ƙofa sukayi kiciɓis da iro wanda yadaɗe da sanin fareeda amma ita bata sanshiba,

Sai dai ganinta da wannan uwar flaster yayi matuƙar bashi mamaki,

Amma dayake shima ya iya kanshi sai atake ya ɓoye mamakinsa tareda cewa,

"sannu baiwar allah"

A hankali ta ɗan ɗaga laɓɓanta da yanayinta zai tabbatar maka kawai tana dauriyane,

"yawwa nagode"

Kawai tafaɗa tareda yin gaba tabarshi a tsaye,

da sauri iro yajawo wayarsa tareda latso layin merry,

Ai kuwa bugu ɗaya ta ɗaga taredayin saurin cewa,

"lafiya dai iro?"

"gata nan ta taho,saidai fa naganta da flaster a goshinta da alama dai wani abu yana faruwa,

Wani ƙasaitaccen murmushin mugunta merry tasaaki,

Duk da dai batasan waye yayiwa fareeda hakan ba amma dai hakan yayimata daƈi sosai,ganin fareedar na tahowwa yasatayi saurin cewa Iro,"ok badamuwa sai munyi waya"tunkafinma ta kashe wayar iron yarigata yin sairin kashewa tareda sake latso wata nmbr da bana ko tantama matar ƈazunce,itama dai bugu biyu ta ƈaga da sallama abakinta kafin iron ya amsa mata tareda fara koro mata bayani,

"ranki yadaƈe yanzu haka daga cikin asibitin nake kiranki kuma naga budurwar zayyad tafito amma fa da alamun anyi mata dukan tsiya sai dai fa bansan wanda yakeda alhakin yin hakan ba,nadai ganta anyimata drasiing na ciwukan fuskarta,"

A hankali me maganar tace," badamuwa iro ni nasan wanda yayi mata amma inason ka bincika min ko zakaga khadija acikin asibitin,dan inada tabbacin khadija ce kaƈai zata iyayin wannan aikin itama saidai inko yarinyar ce tayimata wani abu dan nasan halinta sosai"

to ranki yadaƈe, sai dai fa amma bansan lhadija ba,"

"kanuƈe wayarka yanzu inturo maka hotonta"

"Ok"

A can ɓangaren khadija kuwa tun tana risgar kuka a takure a jikin kujera har ta gaji ta malale akan tiles ƈin office ƈin tanata shaɓaɓa baccinta da yake tafe da ajiyar zuciya tsabar kukan datasha,

To shima dai dr zayyad haka yayi aikin yagama bawani kuzari a tattaredashi saidai abinka da wanda ya yeare ta wannan fannin ansamu sa'ar aikin sosai inda akayi lafiya aka kuma gama lafya,

tunda fareeda ta doshi motar merry ke ƙuramata ido da kallon mugunta saida ya matso sosai kafimn cikin duniyaci merry ta buƈe motar akiƈime tareda kallonta cikin mamaki tace,

"Subahanallahi! sannu ƙawa yadai? meyasa meki haka?"

Har cikin rai fareeda najin daƈin yadda merry ke nuna kulawarta amma duk da haka bazata fasa aniyarta na watsar da ƙawancennan nasuba dazaran tasamu zayyad ƈinta a hannunta dan tasha alwashin ko a bikinsu yan uwan zayyad bazasuga mery a matsayin ƙawartaba barema suyi mata wani kallon yar iska,

ta ɓotan da merry tayine yasata saurin dawowa hankalinta,

"ƙawata ko zayyad ƈinne yayimiki haka?"

A hankali tace,

"Haba dai merry zayyad da dukana kuma!

wllhy wata mahaukaciyar yarinyace ni ina tunanin ko sonshi take ma amma ni banga menayimataba"

Da sauri merry ta karɓe zancen dacewa, "kodai yar uwarsa ce"

"Gsky bana wannan tunanin dan banga wata alama ta hakanba"

"to yanzu haka zamu ƙyale wannan maganar tadakeki amma ba wani mataki"

"Hmmm merry kenan kina tunanin zayyad zai ƙyaletane bayan kuma yasan metayimin? tunima yacilla ta office ɗinsa ya kulleta inaga dai saiya gama aikinsa zai eaiwayi matakin dazai ɗauka dannaga shima yana cikin shirin aikine"

Sosai merry take ƙoƙarin gaɗiye baƙin cikinta da duniyancin tausayin fareedar kafin tace,

"Shikenan amma dai gsky naso ace mu muka ɗauki mataki dakanmu"

" Badamuwa merry na yadda da zayyad a yadda yakesona bazai taɓa batin wani ya takaniba"

Wani sakaran kallo merry tayiwa fareedar tareda faɗawa motat a zuciyarta kuma tace,

"sha'sha'sha kawai"

itama fareeda motar tashiga ta zauna da ƙyar alamun jikinta yafara tsami,

Sai kusan magarib kafin zayyad yanufi office ɗinsa a gaggauce har yanzu zuciyarsa na riƙe da abinda yafaru,

mukulli yasaka ya buɗe office ɗin a hankali ya tura yashiga,

Sosai yayi mamakin yadda yaga yariyar kwance akan tiles tanata shirga bacci kamar babu abinda yadameta,

jɓtsayiwa yayi a kanta yana ƙaremata kallo duk da bawai sosai yake iya ganin fuskartaba,

Sai dai kuma jin yadda take sauke numfashin wahala da wata shahhekar kuka yasan da alama bataji daɗin kwanciyarba ga kuma yadda gabaki ɗaya tabi ta duyunƙune jikinta acikin hijabi,

A hankali yakai hannunsa ya fara janye cukui kuyen datayiwa fuskarta,

da dabara yasamu gyara mata hijabin tareda ƙurawa kyakkyawar fuskarta idanu,

A karo na farko daya nutsu da kallon tsarin fuskar mutum da tsanfsar kyau,

A gsky kyawun halittar fuska baifiya birgeshiba kamar yadda kyawun tsarin jiki ke ɗaukar masa hankali,

Sai dai a yau karon farko yaji kyawun fuska ta birgeshi yakuma ɗauki hankalinsa sosai fiyeda yadda kyaeun jikin da tsarin halitta kan ɗauki hankalinsa,

har yau yakasa gaskata abinda zuciyarsa keyimasa a lokuta da dama na shekaru masu tarin yawa,

Dyk da yasan zuciyarsa akan daidai take amma bazai taɓa gaskata ta ba koda yasan abinda take buƙata baitaɓa zama haramun agaretaba amma shi yana ɗaukar abin a matsayin ƙasƙantar da kai,

duk yana zntukannan da zuciyarsa ne yayinda yake ƙurawa fuskar khadijan idanu datayi fayau da zanen shatin ruwan hawaye akan ta,

Shi kansa ya tabbatarwa kansa khadija kyakkywace sannan kuma tanada diri mai ɗaukar hankali fiyeda tunaninsa,

A hankali yakai hannunsa daidai saitin jajayen labbanta tareda ɗora yatsansa,

taishin dayajine yasakashi lumshe idanunsa tareda sake ƙoƙarin murzawa,

A hankali laɓɓan suka fara motsi da alamun a ddu'a takeyi ,

Ko kafin ya ankara ta buɗe dara'daran idanunta fess akanshi,

Firgigit ta miƙe tareda fara ja da baya cikin alamun tsoro,

shi kuwa zayyda idan ka klleshi zaka iya rantsewa bashi bane yanzu yagama susuta akan kallon fuskarta ya wani haɗe rai kamar bai taɓa dariya ba,

ƙara gyara tsayuwarsa yayi tareda harɗe hannuwansa akan ƙitjinsa yacigaba da ƙureta da mayun idanunsa,

A zhiri fuskar zayyad zaka iya rantsuea mummunan fushine akanta da kuma ysabar tsanar khadijan,

Sai dai kuma a baɗini wani yanayine daya ɗauki dogon lokaci yana masa yawo da gizo yake daɗa ninkuwa acikin zuciyar tasa ,

Ya nada tabbacin abinda yarinyar tayimasa zai sakamasa tsanarta,to amma meyasa kome takeyimasa bayajin wannan tsanar saina wani yanayi daya kanji wanda yake namijin ƙoƙari wajen dannesa,

tuno yadda sukayi ɗazu yasa wani ƙayataccen murmushi ya kusan suɓucemasa,

amma yayi wata muguwar dakiyar hana murmushin fallasa asirinsa tareda sake murtuke fiskarsa,

A hankali yafara takowwa yazuwa inda take,

A kiɗime ta fara bashi haƙuri cikin zazzaƙar muryarta tareda buɗe baki da niyyar zunduma masa ihu,

da sauri ya ɗaura yatsansa alan laɓɓansa tareda yimata shhhhhhiiiiiiii,

Aikuwa a take ta rufe bakinta da tafukan hannayenta dasuke ɗauke da maroon ɗin ƙunshi tareda haɗoye kukanta,

Saida yazo dab da ita har numfashinsu na bigun juna kafin ya ɗauki hanninsa ya ɗaura kan bango dayake yafita tsayi sai yayimata rumfa da faffaɗan ƙirjinsa,

Sun ɗauki dogon lokaci ahakan kafin a hankali ya buɗe bakinsa cikin wata murya mai wuyar fasaarawa yace,

"khadijar"

D a ƙarfi amon ya daki dodon kunnenta,batamasan sadda ta haɗiye wani arnen yawuba tareda jin wani rugugin duka da ƙirjinta yayi,

A karon farko a duniya taji yaya zayyad ya kira sunanta,kiranda tunda aka haifita babu kiran data taɓaji sama da wanda yayimata a yau,

Dama haka yaya zayyad ya iya kiran sunanta? zata iya rantsuwa a duniya babu wanda ya iya kiran sunan sama da yaya zayyad ɗin,

hmmm dama haka ya iya kiran sunanta amma ahine dan baƙar mugunta bazai iya kiranta dashiba sai dai ya ringa cemata wani ke kamar ɗiyarsa ta fari,

nannauyar ajiyar zuciyar dayasaki mai tafe da iska ce ta mai dota cikin hayyacinta,

Aikuwa a razane ta ɗago idanunta,karaf suka faɗa cikinnashi kamar anyimusu trasfer zayyad yaji wani abu yafito daga idanun khadijar batareda ya ankaraba yashige cikinnasa idanun,

Lumshesu yayi a hankali tareda buɗewa,

Wani yanayi yaji mai kamada an karyamasa gabaki ɗaya garkuwar jikinsa,

A hankali yasauke hannunsa tareda ƙafafunsa baya a hankali gabaki ɗaya ki yake kamar anyimasa duka,

Cikin takunsa maikamada na maiyin sanɗa yaja ƙafafunsa tareda ɗaga laɓɓansa a hankali yace,

"muje gida"

yanajin lokacinda ta sauke wata nannauyar ajiyar zuciya tareda cewa masha allahu,

bai wani ysaya saurarentaba kawai wayarsa ya ɗauka da laptop sai mukulli,

Ganin yadda jikinsa yayi sanyi sai kuma khadijan taji duk aba daɗi koba komai dai ɗan uwantane kuma sai takeji ajikinta kamar ya muzanta,hakan datajine yasata saurin kai hannunta ta karɓi jakar laptop ɗinsa daga hannunsa,

jin ta kama jakar yasan nufinta tunda ya tabbatar itaɗin tarbiyyar ammi ce hakan yasa ya sakarmata tareda miƙa mata wayarsa,

kallonsa ta ɗanyi kafin ta karɓa

A hankali ta taɓe bakinta a ranta tace,

"mugu dai bazai taɓa canzawa ba, watakam ga par dako?,

Ganin ya fita yasata fitowwa da sauri shima ya rufe office ɗin suka nufi parking space.....YAR MUTAN MURAYE GARKUWAR MUTANEN DAURA ALHERIN MUTANEN MASHI,😎😆😉RAƁA DANNIN MUTAN KANO34&35

A can gidan kuwa tunda akan sallami su ammi aka koma gida gabaki ɗaya gidan ya hargitse da murnar dawowar ammi daga asibiti,

to dayake da yamma ne yaran gidan na kowwa yana gida haka aka haɗu a parta ɗin ammi anata hira da yimata sannu,

Koda ciwon ammi yakasance na marasaa son hayaniya amma tanajin daɗin kulawar da yan gidan ke bata,

Musamman ma yanzu da aka haɗu a part ɗunta anata shan hira hadasu hajjaju,

Ana tsaka da hirarne ma yan ɗanbatta suka zo haba nan fa aka shiga hira dayake gabaki ɗayansu sukazo aunty shamsiyya yaya shms yaya faisal dakuma noor,

Tunda sukazo yaya shams yake neamn par uwarsa watam khadija dan a zahirin gaskiya kowa yasan shayuwarsa da khadijar dakuma shirin daauke yi sosai,

Dan yaya shams mutum ne lan gayu mai kuma taƙama da aji da gayunsa,

To itama gogan taku aminatu dai tun ɗazu take baza idanu dakuma tambayar inda khadijan ta tafi duk da dai su yan gidan sun zata har yazuwa wannan lokacin tana makaranta,

Amma ganin har yamma tayi sosai sai aka fara tunani kota wuce aaibitinne kasancewar babu waya a hannunta,

sosai hankalin aminatu yasake tashi jin ance khadija na tareda yaya zayyad tuni wata mugiwar tsanar khadijan tasake baibaye zuciyar aminatun gsky dolene ta nunawa khadijar kuskurenta kida kuwa hakan zai kasancewa silar watsa duk wata kyakkyawar alaya dake cikin a halin dolene zata mallaki burin zuciyarta watau yaya zayyad,

Ganin anata jajanta shirun khadijar yasa aunty maimuna ɗaukar wayarta ta kira yaya zayyad wanda a lokacin fitowwarsa kenan daga aikin tiater dayayi,

ganun wadda ke kiransa yasa ya ɗauka cikin ɗan sakin fuska ya amsa sallamarta kafin ta fara magana,

"zayyad wai dama ko khadija ta zo nan asibitinne dan ba waya a hannunta kuma batasan ansallami ammi ba gashi har yanzu kusan magrib bata dawoba"

Sai da takai ƙarshen maganarta har ta ɗauka ma bazai yi maganaba kokuma layin ya tsinke kafin can taji ya fara magana,

"kayyy auntynmu gsky ki ringa ragewa mana,haba tunda kika ɗauko zance kin ƙi saukew,ok ni baku damu daniba tun jiya bana gida amma yanzu kun kirani saboda wannan farfeluwar yarinyar ko?"

a hankali aunty maimuna ta saki wani tattausan murmushi wanda yake daidai da saukar mashi ko takobi a ƙahon zuciyar mama dakuma aminatu kafin taci gaba da cewa,

"haba babban yaya aikai uba ne kuma ƙaton tuzuru kaga kuwa bakada wanda zai nemeka"

"hmmmm aunty kenan,ok tunda gaka ne itama wadda kike nema ai batada aure kinga kenan kinyi sonkai"

"Dr zayyad kenan ko dai khadija batada aure ai natabbatar tanada wanda zai haukace da nemanta muddin kuwa akace ta ɓata ƙilama daga ranar yadaina cin abinci"

"to indai hakanne nima ai inada budurwa,"

"hmmmn ai budurwa ba dahir bace"

"kinga kenan itama saurayi ba dahir bane dan haka one'one"

"Hmmn to kasani ita ko ba saurayine zai nemetaba?"

Aunty maimuna tayi wannan furucin cikin comfidence ɗinta kafin yaya zayyad ma cikin ƙardin gwiwarsa yace,

"to waye zai nemeta faɗamin aunty"

"kaine!"

lafazin daya daki zuciyoyi da dama musamman daya kasance gabaki ɗaya falon kowwa hankalinsa da sauraronsa yana kan aunty maimunar da muhawarar ta da yaya zayyad ɗin,

"ni kuma!"

"ƙwarai kuwa kaine zayyad!"

Auntyn tafaɗa da ƙwarin gwiwa kafin ta cigaba da cewa,

"ka manta babban wa uba!kaga kenan idan khadija ta ɓata sai kafi kowwz shiga tashin hankali shin kagayamin kai wanene yayanka?"

zukata da dama sun sauke ajiyar zuciya sai dai kuma kowwa da inda tashi ta dosa musamman mama da aminatu sai kuma yaya zayyad kafin yacigaba da cewa,

"wallahi aunty maimuna bakida dama,toshikenan tunda banada yaya idan naɓata ai zakifi kowa jin jiki musamman ma ace mutuwa nayi"

"gsky kam zanfi kowwa amma bazanfi khadija ba saboda ita tarasa jigo"

ƙit ta katse wayar tabarshi da waya a hannunsa wanda sai da ya daɗe yana juyata kafin yanufi office,

Itama aunty maimuna tana sauke wayar ta kallesu da murmushi kafin tace,

" ba damuwa tana tareda yaya zayyad"

jin kiran sallar magrib yasa suka fara tashi dan sauke faralinta akan lokaci,

a hankali suke tafiya har suka ƙarasa bakin motar yaya zayyad,

ɓangaren driver yazauna wanda sanin halinsa yasa ita ma ta buɗe mangaren mai zaman banza ta zauna,

sai da tayi addu'a kafin yayiwa motar key ya daidaita ya fara tafiya a hankali kamar wanda akayiwa duka,

Sunyi nisa sosai da tafiya amma motar ta ɗauki shiru kowwa da abinda yake ayyanawa acikin zuciyarsa,

Musamman ma yaya zayyad dayakejin wani yanayi mai wuyar fasaarawa,dan bazai taɓa cewa acikin farinciki yake ko baƙin ciki ba,

S hankali yakai hannunsa tareda murɗa radion motar ya kunna ƙira'ar sudais ya fara bi cikin wata iriyar murya mai fiddda nagartaccen amo,

Sosai yanayin da ya canza na saurarar ƙira'ar sudais dakuma amon muryar dr zayyad yayiwa khadija daɗi wanda hakan yasa takejin wani sanyi na ratsa zuciyarta da dukkan gaɓɓan jikinta,

cikin mintunan da bazasu gaza boyar zuwa shidda ba wani daddaɗan bacci yayi awob gaba da ita,

A hankali kanta ya gangaro zuwa kan kafaɗar yaya zayyad wanda ita kanta batasan da faruwar hakan ba,

Shi kansa yaso ture kannata daga jikinsa amma ya rasa meyasa ya tsinci kansa da sake gyara mata kannata ya wani sake jawota a hankali cikin dabara ya ɗora kannata akan ƙirjinsa,

Gaba ki ɗayansu suka sauke ajiyar zuciya sai dai kowwa da manufar tasa ajiyar zuciyar,

har ga allah khadija tayine dan jin daɗin kwanciyar da tayi bawai dan tasan ki a jikinws takeba,

Saɓanin dr da shi kuma tasa yayine dan jin khadija a jikinsa da wani ni'imtaccen ƙamshin daya daki hancinsa,

A hankali yake driving da ɗayan hannunsa yayinda ɗayan gannun yake akan kafaɗar khadija dayake ɗan wasa dashi a hankali,

Canza salon tafiyar dayayine yasa suka ɗan ɗauki dogon lokaci kafin su isa gida,

Lokacin da suka iso anata kiraye kirayen sallar issha hakan yasa yasamu guri a gefen motar abbansa yayi parking amma yarasa me yasa ya kasa tada khadijar barema yake yasamu jam'in sallar issha dayakeji,

Sun kai minti ishirin a haka yana ganin su abba da sauran iyayensa da yaran gidan maza na ta shiga gida amma hakan baisashi ya tashi khadijar ba,

ko minti biyu ba'ayi da shigar su abban ba kamar an mitsini khadija ta farka da addu'a a bakinta tana murtsuka idanunta,

Kamar a mafarki ta jita kwance ajikin mutum aikuwa ta sake murje idanunta amma still fai ta sake jinta ajikinsa,

Da sauri ta yi azamar miƙewa zaune saidai yakasa bata damar hakan kasancewar gabaki ɗaya yayimata dabaibayi da hannuwansa,

Duk yadda taso ƙwacewa ta kasa hakan yasata sakarmasa wani maranyan kuka,

A hankali cikin salo ya wani mirginota takoɓa daidai suna fessing juna kafin ya ɗauki hannunsa ya ɗaura a laɓɓansa tareda yimata shhhhhhi,

aikuwa da sauri ta haɗiye kukanta,

Hannunsa ya zira cikin aljihun wandonsa ya miƙomata ɗan ƙaramin hanky mai kyau sai ƙamshi yake,

Sanin abinda yakr nufi yasata saurin karɓa tareda fara share yɷan kwallanta dasuke niyyar gangarowwa daga idanunta,

Da kansa ya ɗauke hannunsa daga kikinta tareda taimakamata ta tashi daga jikinsa,

aikuwa da azamar ta ta kama murfin mitar zata buɗe,

Da zafin nama ya wani fisgota ta sakw faɗowwa jikinsa tareda haɗe bakinsa da nata guri ɗaya yafara aikin tsotsa dan dama har ga allah dauriya kawai yakeyi ,

Ssai take mutsu mutsun ƙwacewa amma innnna hakan ya gagareta har saida yayi nasarar saka hannunsa ya kamo nonta ya fara murzawa da ƙarfi,

jin abinda yafarane yasata sadaƙarwa dan tasan bazata taɓa iya ƙwatar kanta daga wannan maitar ta yaya zayyad ba,

Yo inba maitaba me ace mutum bashida iaki sai shan bakin mata,

Shi kuwa gogannaku jin ta saki jikinta yasa yacigaba da tsotsar harshenta da yakamo ta ƙarfin tsiya tareda saka ɗayan hannunsa ya yaye hijab ɗin dake jikinta ya maidashi baya tareda sake maida hannunsa ta bayan ya zuge zip ɗim rigar,

Aikuwa kamar jira rigar take ta faɗo daga ƙirjinta zuwa ƙasa,

Tuni push up bra ɗin datasaka ta ƙara ƙawatawa dr zayyad zayyad tsantsan cika da kyawun tsayuwar nonuwan khadijar,

Aikuwa ba ɓata lokaci yasakw kai hannunsa yafara shafa samansu a hankali kafin yazare bakinsa daga nata tafara lasar wuyanta da saman ƙirjinnata cikin wani salo mai kashe jiki,

Salon da yafara mantar da khadija ainahin halin da ake ciku dan har fa alkah dr zayyad gwanine a fannin ruɗa kowacce irin mace musamman yadda yake tafiya da salonsa na ɗaukara hankali da iya tafiyadda kowacce irin mace,

Bata ankara ba taji ya jaiwa kan nononta wata iriyar cabka da wani salo na kashe wanda akeyiwa,

Aikuwa ta daddage tasakar masa wani wahalallen nishi a daidai saitin kunnensa,

nishin da yasoya canza salon tafiyar zuwa wani salo na musamman dan har ga allah nishi ba yaramin tada hankalin zayyad yakeyiba,

Sai dai kuma a lokacin da salon yaso canzawa a lokacinne kuma wayar dr ta fara neman agaji da salon kiramda ko a wanne hali yake dolene yabawa wannan kiran dama ta musamman dan ring na daban yasaka wa mai kiran,

A hnakali ya zare bakinshi daga cikin bress ɗin khadija da wata kasala ɓai kamada anyimasa dukan tsiya yanjawo wayar kuma alokacinne kiran ya tsinke,

sai dai kuma sanin baza'a sake kiranba yasa ya danna kiran layin,

Aikuwa bugu biyu aka ɗaga ciki sasaanyar murya ammi ta fara magana,

"ɗana kayi haƙuri jin bankitaka ba wllhy gidabne acike da mutane ya aikin'

Cikin kasalalliyar murya yafara magana,

"sorry ammina ya jikinnaki?"

"da sauƙi sosai ya aikin"

"aiki alhamdulillah,"

"yawwa madallah,gameda allurata shine babanku yace tunda aiki ya tsareka ko nan zamuzo sai kayimin,"

murmushi ya ɗan saki yareda kallon manfarenda khadija take ta wutsiyar idanu a ransa yake ayyanawa,

Allah sarki ammi bazata taɓa tambayarsa khadija ba shin anya kuwa yanayiwa rayuwar ammi adalci kuwa,

cikin sauri ya kawadda zancen da wani radaɗi a zuciyarsa kafin yace,

"aa ammi kinganni ma yanzun na shigo gida ,"

"ok har naji daɗi wllhy dan banason kasake kwana a asibitin yauma wllhy"

Wani murmushi yayi da saida ammi tajiyo sautinshi kafin yacigaba da cewa,

"waneni insake kwana uwata ba lafiya ainama ɗauki hutun sati guda najinyar mahaifiya"

itama murmushin tayi tareda cewa allah yayimaka albarka,

"amn ammina"

Tana katse kiran ya kai dubansa ga khadija da tuni ma ta gyara shigarta nml kamar ba itaba,

kallonta yayi a tsanake kafin yace,

"diyyar jinin budurwata nacire da kika zubar mata kuma duk ranar dakika sake sainayimiki abinda tafi haka yanzuma ki gdewa allah"

To dai khadija babu bakin tsiwa amma da sai antaɓa,

A haka dai suka fito suka nufi gida gabaki ɗayansu kamar wayanda ƙwai ya fashewa,

Sanin yazuwa yanzu duk ana falon hajiya har iyayensu yasa shima dr zayyad yanufi part ɗin hajjajun,

A tare suka yi sallama aka amsa kanar yadda sukayi tunani kuwa gabaku ɗayansu suna part ɗin hajiyar harda mutanen ɗan batta dayake kwana zasuyi,

Jun muryar khadija yasa yaya shams dayaketa faman chat yin saurin ajiye wayar tareda miƙewa ya ti wajen khadijar yana,

" Oyoyo my sister"

To itama khadijan jin muryar yaya shams yasa duk wani fishi na fuskarta ɗaukewa kasancewar sun kwana biyu basu haɗuba yasa itama da gudunta ta nufi yaya shams ɗin,

Kasancewarta mai cikakken dirarren jiki yasa yadda take murnar gabaki ɗaya ko ina na jikinta yake motsawa musamman sharp ɗin ƙugunta,

Ganin hakan yasa zuciyar yaya zayyad tafara wani mahaukacin ta farfasa da zugi gakuma wani tsananin fishi dake axalzala zuciyarsa,

wata mahaukaciyar tsawa ya daka musu wanda saida gabaki ɗaya part ɗin hajjajunya amsa amon muryar zayyad ɗin,

cikin hanzari yaya shams yaci wani uban birkin da saida ya kaishi yin tuntuɓe da ƙafar baba ummarun,

Gaba kiɗaya falon yayi tsit kowa da abinda yake ayyanawz acikin zuciyarsa,

Amma duk yadda zayyad yayi wannan ywar tsawar hakan bai hana khadija ƙarasawa kusada yaya shams ba,

Sai dai kuma amaimakon rungumeshi datayi niyyar yi saita kama hannunsa duka biyun ta riƙe tareda ɗora kanta ajikin kafaɗarsa,

duk da kasancewar bata rungumeshiba amma hakan bai hana zuciyar dr zayyad sake ingizashi cikin fishi ba tareda rufe idanunsa dazazzafan kishim daya kasa gaskata zuciyarsa da kishin khadijar yakeyi,

da wani azababben fishi ya finciko khadijar tareda ɗaga hannunsa ya wankawa shams wani rikitaccen mari,

Jin ƙarar marin saida gabaki ɗaya hankalin mutanen wajen ya tashi cikin kiɗima da gigita yaya shams ya ɗago hannunsa riƙeda kuncinsa,

Wani zazzafan hawayene yake fita daga idanunsa na dama,

Sai dai kuma duk yadda yakai da shiga cikin fishi da gigitar marin hakan bai hanashi hango wutar bala'i da masifar mugun kishi ba a idanun dr zayyad ɗinba,

Duk da kuwa yadda ya kasance darene amma dayake da isasshen hasken lantarki hakan ya bada damar kowa naganin kowwa tsab,

Dr zayyad kuwa cikin wani azababben kishi yafara magana,

"ashe dama bakuda hankaki bare tunani,idan ita sakaryace kai ina hankalinka da tunaninka,shin abinda kayi kana ganin daidaine ko kyautawa!to wllhy na rantse maka da Allah wannan shine na farko kuma na ƙarshe duk ranar sa nasake ganin irin haka wllhy sai ka gane kurenka,"

Da tsantsar fushi yasake kai dubansa ga lhadija tareda daka mata tsawar da tasakata tsorata,

"zaki wuce ko saina ɓallaki"

Ya faɗa tareda nuna mata hanyar ɗaki,

Aikuwa da gudu ta nufi hanyar ɗakinta,

Kafin shima a fusace ya nufi part ɗinsa da wani razanannen fishi,*DR ZAYYAD*

PAGE 36&37

NA

HAJARA MURAYE

(*MRS AMINULLHY)*

SADAUKARWA

MURAYE FAMILY

_____ga baki ɗaya fa wuta ta ɗaukewa lowa aɗakin musamman ma iyayensu da gabaki ɗayansu suke auna abinfa zayyad ɗin yayi a ma'aunin hankali da mizanin tunani,

Aɓangaren mama kuwa sosai ta faɗa cikin shakku da tunani, kawo yanzu dai ko tantama ba tayi ta san ba shakka zayyad na son khadija koda kuwa bai faɗa ba,

Shin me hakan yake nufi!?

cab aikuwa wllhy bazata taɓa yadda da wannan lamarin ba dolene ma zata tabbatar ta yi yadda tayi ta raba tsakanin zayyad da khadija koda kuwa ta halin ƙaƙa ne sannan kuma ta aurawa zayyad ɗin ɗiyarta koda hakan zai zama sanadin raba zumunci,

a hankali Baba ummaru ya sauke wani gauron numfashi tareda kallon shams da har yamzu yake riƙe da kunci,

har ga Allah shi kansa baba ummarun yanzu ya fara sarewa da al'amaron zayyad,ya kawai mutum zai ɗauki hukunci ba tareda ya nisar ko yayi faɗa ba,

Ganin kamar baba ummaru ya kasa magana ne yasa ɗan uwansa baba safiyanu yin magana cikin ƙwarin gwiwa,

"tun a yanzu ba tareda anje ko ina ba Allah ya nuna mana munada magajin da zai riƙe amanar bayan mu ya bawa bayan mu tarbiyya fiyeda yadda zamu basu yakuma kula da bayanmu,"

Sai da ya ɗanyi shiru yaja numfashi kafin yaciga ba da cewa,

"haƙiƴa yau nayi alfahari da zayyad dakuma abinda ya aikata ɗari bisa ɗari,musamman yadda ya ɗauki hukunci a gaban idanunmu dan nuna mana yadda muke ganin irin wannan kura'kuran amma muna kauda idanunmu muna nuna ba komai bane,Allah yayi masa albarka ya bashi mata ta gari"

ga baki ɗaya falon aka amsa da amn kafin yasake kai dubansa ga yaya shams,

Kai kuma shamsu karka ɗauki abinda zayyad yayi maka da wani fuska ƙaunace tasa yayi maka dan haka idan ya huce kaje kabashi haƙuri"

A hankali yaya shams yace,

"insha allahu abba,"

"Yawwa ai dare ma ya soma yi dan haka zamu iya tafiya kowwa yaje ya kwanta allah ya tashemu lafiya,"

Gaba ki ɗaya aka masa da amn kafin kowwa ya fara neman hanyar fita,sai mutanen ɗan batta kawai da zasu kwana a part ɗin hajjaju,

A ɓangaren oga zayyad kuwa tunda ya fita da wannan fushin bai zame ko inaba sai part ɗinsa,gaba ki ɗaya zuciyarsa a jagule take da damuwa a haka ya shiga wanka yana ayyyanawa a ransa,

"gsky wannan yariyar batada tunani bare hankali,inba rashin tunani ba ace ke bazaki taɓa sanin kin girma ba?,"

haka dai ya ringa saƙa zantuka a ransa har yagama wanka ya fito a gaggauce ya shirya jilinsa cikin riga t shirt da gajeren wando tareda saka turaren miziyan mai sassanyan ƙamshi,

kafin ya shimfiɗa dadduma tareda gabatar da sallar magarib da issha,

yana ƙarasawa ya ɗauki wayoyinsa ya nufi ɓangaren ammi,

Da sallamarsa ya shiga,ya samesu a falo igaba ki ɗayansu mamman'ummy dakuma maryam sai ammin da abba,

maryam ce tayi saurin miƙewa tareda nufarsa da gudu,

Aikuwa da fara'arsa ya cafe ta tareda ɗaga ta sama ya fara juyi da ita,

Da fara'a ammi take binsu da kalli kafon tafara magana cikin raha,

Wllhy kasauke ta itama dayake batada tausayi zata wani ɗareka bayan yanzu ka dawo daga aiki a gajiye,"

Ganin basu tankataba yasa tayiwa maryam ɗin magana a ɗan tsawace,

"wai bazaki sauko daga jikinsaba saikin karyamin yaro"

A hankali dr zayyad ɗin ya sauke maryam yana fara'a da jin gabaki ɗaya damuwar datake tattare dashi tana barinsa,

Gsky ammi uwace da duk wanda yasameta dolene ya godewa allah,

A kan kujerar 2seater da abba yake zaune ya zauna tareda sake gaisheda abban da shima yajeyiwa dramer su dariya,

Yaya mamman ne yasake gaisheshi tareda muƙewa yayi waje,ummy ma gaisheshi tayi tareda miƙewa zata shiga ɗaki,

"ummy ki ɗaukowa yayanku abincinsa kafin kishiga ɗaki"

amsawa ummy tayi tareda ɗan kallonsa tace,

"yaya insauko maka dashi ko na yi saving adining"

Kamar bazai amsaba haka yaɗan ja iska kafin yace,

"ki kawomin nan,"

A ɗan hanzarce tayi hanyar dining dan cika umarninsa

Falon ya rage daga shi sai abba sai kuma ammi kasancewar maryam tabi ummy,

Abba ne ya kallesa da alamar maganar dazaiyimasa tanada muhimmanci,

Hakan yasa ya maida hankalinsa gabaki ɗaya kan abban,

"zayyad?"

"na'am abba"

"Watakam ɗazu kayi wani hukunci wanda banji daɗinshi ba kuma sai nake ganin kamar bakayi tunani ba ka yanke hukuncin da kwata kwata ba shi yadace kayiba,bawai nace abinda kayi baiyi daidaiba a'a ko kaɗan saima gyara danakeson yimaka kasancewar kaine babban uba wataran a gidannan,"

Sai da abban yaɗan nisa kafin yacigaba da magana,

"Bawai shams ya dace kayiwa hukuncinba face yarinyar da abin yafaru a kanta duba da ita tafi shams laifi saboda ai itace ummul aba isin komai dan haka a kiyaye gaba,"

Tunda ya fara magana kan zayyad yakr a duƙe sai yanzu da yakai aya jafon dr zayyad ya ɗan ɗago kansa tare da cewa,

"angode abba Allah ya ƙara girma"

"Amn amn allah ya tsare"

miƙewa shma abban yayi tareda yimusu saida safe yanufi ɗakinsa,

a hankali suke ɗan taɓa hira tsakanin zayyad da ammi yana cin abinci har ya gama tayi mata allura tarda bata magunguna,

Sai da ya tabbatar ta shiga ɗaki kafin ya nufi part ɗinsa ya keanta,

Tunda ammi ta shiga ɗaki take tunanin tattaunwar dadyn da zayyad a ranta tasan dole ko dadyn ya ɓoyemata to ba shakka akan khadijane saboda ko bata san me yafari ba tadan a gidan babu wanda yake shiri da shams sama da lhadija,

inkuwa hakane tabbas akwai abinda yake faruwa wanda batada hanyar jinsa tadai san koda ace wani abune babba bazasu taɓa faɗamata ba saboda yanayin ciwonta,

A haka dai taketa tunane2 kafin ta yanke hukuncin dolene zata jawo yarta jikinta sosai dan gudun danasani dakuma nunamata yadda rayuwa take kodan gaba saboda ta tabbatarwa kanta rashin wayau na damun rayuwar khadija,tunda har yanzu da sauran yarinta a kanta,

Haka dai ammi tayita tunane2 kafin ta tashi ta ɗauro alwallah ta fara kaiwa allah kukanta,

A ɓangaeen khadija ma tinda ta shiga ɗaki take sharɓar kuka dakyar ta tashi ta ɗauro alwallah tayi sallar magrib da issha kafin tasha magani taɗan kwanta a kan dadduma,

aikuwa tuni wani bacci mai nauyi yayi awon gaba da ita daƙyar ma aunty shamsiyya data shigo zata kwanta tasamu ta tasheta ta maida ita kangagado tareda yimata addu'a,

A ɓangarensu merry ma tunda suka tafi fareeda taje famfata akan ciwuwwukan jikinta,

A gsky ƙawata yakamata mu canza wa zayyad salo akan maganar nan musan inda aka tsaya dole fa sai munyi amfani da hotunan nan kafin zayyad ya yadda da maganar aurenku,

Sosai damuwa ta bayyana akan fuskar fareeda,

A hankali ta sauke wani gwauron numfashi kafin ta fara magana,

A gsky merry ina matuƙar son zayyad son da bazan iya tantance ni kaina wanne irine ba,

Hakan yasa banason sainayiwa zayyad barazana akan maganar aurena nafiso na cigaba da nuna masa irin tsantsar son danakeyimasa a haka nasan zai gaskata zuciyata,"

Tunda ta fara magana merry keyimata wani kallo na sannu shashasha!

"gsky fareeda bakida wayau! watakam ke a haka kike tunanin zayyad zai soki ya kuma aure ki ko? to bari kiji wllhy kima farka daga wannan ƙazamin bacvin dakike wannan mummunan tunanin dan zayyad ba ƙaramin tantirin ɗan duniya bane,

Shin ke inkina tunanin samun zayyad a gurinki haka yake da sauƙi wllhy ina dunanin da kin daƌe da samun zayyad da mata sama da guda biyu,dan yadda zayyad ya haɗu haka wllhy na tabbatar da yanada sauƙi gurin samun aurensa da baima sankiba dan da tuni wata ta gama zama matarsa kinga kuwa ko kinsansa badai da aure ko soyayya ba,"

Sosai yanayin maganganunta suka ƙara saka fareeda cikin damuwa dakuma tashin hankali,

A gsky maganganun merry gskyne amma gsky saidai su samu wata hanyar badai wannan ba dan ita gsky bazata taɓa iya biyowa zayyad ɗinta ta wannan hanyarba,

Isowa da sukayi ƙofar gidansu fareedar ne yasa zancen katsewa,

hakan yasa merry cewa,

"Ƙawata ki shiga gida inyaso gobe idan nazo dubaki zamu gama maganar insha allah,"

"Ok ba damuwa nagode ƙawata"

fareeda ta faɗa tareda ɓalle murfin motar ta fito tayi cikin gida,

"sakarya kawai!merry ta faɗa tana wtsawa bayan fareedar wata muguwar harara tareda yiwa motarta key ta nufi gida,

***

A haka rayuwa tayita tafiya kullum khadija na shiga part ɗin ammi dubata tareda ɗan kama mata aikace aikacenta,

hakan yasa ammi sake jaan khadija ajiki tana sake kwatantamata yanatin rayuwa dakuma yanayin mu'amaka da al'umma musamman daya kasance tanada sura mai ɗaukar hankali,

Sosai khadija taa fara sabawa da rayuwa da ammi da jin daddɗin zama da ita musamman yadda ta fahimci amminta na matuƙar Sonta,

Itama ammin sosai ta fahimci akwai abubuwanda bazata taɓa oya raba kjadija da suba musamman son jiki dakuma da kuma ahagwaɓa,

Khadija bazata taɓa iya zama a kusada mutum batareda ta raɓeshiba hakan yasa duk lokacinda suka zauna da ammi sai ta shige mata tun tana raɓa jikinta har a hankali sai kiga tayi ɗare2ajikin ammin,

a yanzu sosai take kiyaye abinda zaisaka ta keɓe da zayyad ɗin duk da yanzuma suna yawan haɗuwa sosai amma babu abinda yake haɗaau sai gaisuwa duk da har yanzu tana kama yaya zayyad ɗin da satar kallonta amma bata ɗauki hakan da wani abuba saboda bata saka komai a zuciyarta gameda hakan,

****

To a ɓangaren su mama babba ma har yanzu aminatu na nan da soyayyar yaya zayyda a zuciyarta saima abinda ya ƙatayin gaba,

Inda yanzu salo ya canza sosai aminatun take shsshigwwa yaya zayyad ɗin dan yanzuma ta laƙabawa kanta kullum saitaje ta gyara masa ɗakinsa ta turareshi da turaen ƙamshi amma hakan baitaɓa sakawa yaya zayyad ya fahimci abinda take nufiba,

Haka kuma ta ƙaƙabawa kanta zama a part ɗin ammi kulkum musamman ma idan yaya zayyad ya kusa dwwowa daga gurin aiki,

Sosai shisshiginta yake ɓatawa khadija rai dan yanzu ta gama fuskantar abimda aminatu ke nufi saidai ita a gsky bataga abinso a gurin yaya zayydɓad ba,

Ba wai tace yaya zayyad bashida kyau ko qualities ɗin daza'a soshiba a'a,

Ita kanta tasan yaya zayyad mutum ne da mata dayawa sauke buƙatar kasancewa dashi duba da yadda ya yayi ta ko ina,

Amma ita sam yaya zayyad ɗin baya birgeta ko kaɗan saboda bashi acikin irin jerin mazajen datake buƙatar aure, musamman ma yadda yake da raini dakuma disgi uwa uba kuma halayensa da kwata kwata basuyimata ba,mutum sai shegiyar masifa,

"mtsssss"

Ta ja wani mugin tsaki a zuciyarta,itafa anacewa mace tana canza namiji amma ita kanta tasan duk wadda ta auri yaya zayyad wahala kawai zatasha dan bazata taɓa iya canzaahiba,musamman na ace su samu wadda taje mutuwar sonsu kamar aminatu,

tabbb ai wllhy zatasha wahala,hakan yasa ma yanzu dazaran lokacin dawowarsa ya yi take barmusu part ɗin ta nufi part ɗin aunty maimuna,

YꞌAR MUTAN MURAYECE ALHERIN MUTANEN DAURA GARKUWAR MUTANEN MASHI 😀😁😜😝😛RAƁA DANNIN MUTANEN KANO*DR ZAYYAD*

38&39

NA

HAJARA MURAYE

(*MRS AMINULLAHY)*

SADAUKARWAR

TEAM KHADIJA

kamar dai yau data kama alhamis kuma yakasance da yawan yꞌan matan gidan basa makaranta hakan yasa yau ma khadija tunda ta tashi bata komaba ta fara gyara ɗakinta kamar ko wanne lokaci ta wanke bayi kafin ta nufi babban falon hajiya,

kasancewar jiya ansha fira sosai an ɗan ɓaɓɓata falon dayawa yasa taɗanji ranta babu daɗi amma dayake tasan dolene a kanta yasa ta fara aikin tanayi tana mita,

ta gama tattare komai zata fara shara hajjaju ta fito daga ɗakinta da tarin yar kwalemar maganungunan gargajiyarta datayi na cover,

kasancewar fakan sharar yacika tsautsayi yasa hajiya zubarda ɓurɓushin magani akan kafet dake tsakiyar falon wsnda khadijan ke niyyar duƙawa ta nannaɗe kafin ta fara sharar,

har ta buɗa baki da niyyar gaisheda hajiyar amma ganin hakan yasata canza akalar maganar tat cikin ɗan faɗa,

"Gsky hajiya bakya kyautawa abinda kikeyi,yanzu fisabilillahi bayan ɓata falonnan dakukayi jiya duk bai ishekiba saikin haɗa da zubarda shara da gangan haba hajiya kamar dai ba'a tausayina,"

Ta idashe maganar da shagwaɓa,

Tunda ta fara maganar hajiya tayi sararo tana kallonrta har sai da takai aya kafin hajiyar ta yi mata wani kallon tsaf tareda kama haɓa ta fara magana,

"ohhhh ba shakka wata kam gani sarkin ƙazamai ko? lallai hadiza wllhy kinsamu yaɗanci,watakam dan kinga kwana biyu na hana zaidu akanki shine zaki fara tatamin ruwan fetsara ko?"

"Ni wllhy hajiya lamarinki na bani mamaki kamar bake bace kikace indai kincika ke lika haifi ubana bazaki sake kiran suna na ba amma wai abin mamaki kin kasa cikawa,"

Khadijar ta faɗa tana ɗan taɓe baki kafin taci gaba,

Ko danma akan mema zan ta wannan haƙilon bayan na tabbatar wllhy hakiya ko rayukan mutum goma aka baki mudfin kikayi minti goma bakijini ba ko bali kira ni da wannan ruɓaɓɓen sunan ba wllhy sai kin mutu"

Itama hajiyar a rene ta yi tafi tareda yin yaɗar shewa tace,

" yau naga masifa ni rabi!"

"yo wai ke nan hadiza ji kike inba ke bazan iya rayuwa ba kome?"

"hmmm hajiya kenan,to ai wllhy va takaran ni ba ko suna aka canzamin sai kin ida margayawa,"

Da azama hajiya tasake gyara tsayuwarta kafin tace,

"yo wai hadiza bangabe ma'anar idawa ba yanzun kina nufin kice ni saura ce?"

Wata iriyar daeiya khadija tayi da saida ta kaita ga duyaɗawa,sai da tayi mai isarta kafin tace,

"hmmm gajiya kenan,to keda kina nufin rayuwarki mai tsayice,uhmmm tabbb! aikuwa wllhy ki canza dan kuwa mun kusa shan gumbar ki dan kin kusabin tsohon mijinki,"

"hmmm Allah sarki hadiza!aikuwa duk ranar da na muru na tabbatar sai kinfi kowa yin kuka hakan yasama nake roƙon allah yasa na yi tsawon ran gani na aurar dake ga wanda zai lallasheki ko bayan mutuwata"

I tama khadija murmushi tayi tareda zama kusada hajiya hannunta ɗauke da tsintsiyar data gama tattara shara ta ɗaura kanta a gefen kafaɗar hajiya tareda cewa,

Ai insha allahu ma hajiya bazaki mutu ba muna nan tareda ke masoyiyata,

Wani ɗan murmushi hajiya tayi mai kamada yaro yarone tareda cewa,

"Allah ya shirya minke hadizata"

"Yawwa hajiya in tambayeki mana?

"Allah yasa na sani"

"Wai meyasa bazaki iya kirana da khadija kamar kowwa ba? wllhy banason hadizar nan sunanfa tsaffine"

"To zan koya insha allahu,yanzu dai kije kigama kitafi ki taya ummanju aikinta,"

miƙewa tayi ta nufi hanyar fita ta zibar dasharar kafin ta kwashe tasake zubarwa ta hau moping,

A haka suna ta fira da hajjaju har ta gama duk abinda zatayi kafin ta koma ɗakinta tayi wanka tareda turare jikinta da turaren garwashi kafin ta shirya jikinta cikin wata atamfa mai kyau datasha ɗinkindoguwar riga,

Rigar sakakkiya ce sosai dan gaka bata wani kamata ba kokaɗan sai dai tayi mata kyau sosai,

Gashinta ta taje tarda kamashi ta ɗaureshi can ƙasa sosai kafin ta murza ɗaurin daya fito mata da gashin,

Gsky ko ita kanta tasan tayi kyau dan sosai takeson faranta ran amminta,

Plate shoes ta saka wanda yayi daidai da kayanta tareda da ɗaukar turare tasake shafe jikinta gaba ɗaya,

Aikuwa a take ta fara saki wani fitinannen ƙamshi,

Ganin babu hajiya a falo yasa ta ɗan leƙa ɗakin hajiyar saidai jin alamar motsin ruwa a banɗakin ya tabbatar mata fa cewar wanka take,

Hakan yada bata wani tsaya jirantaba ta fice rɓta nufi ɓangaren umma,

A hanya ta ga aminatu da fateema aikuwa cikin fara'a da sakin fuska ta tarbeau yareda dafa kafaɗar aminatun taba cewa fateema,

" Dama yanzu zanje gurinku mu tafi part lin aunty maimuna musha fira,amma tunda yanzu gaku mu ƙarasa ku rakani ingaisheda su umma da su mama,"

Kawai gani tayi aminatu tayimata kallon banza tarrda ture hannunta a fisace ta kalki fateema,

"dallah fateema kizo muje inkuma bazakijeba ni inyi tafiyata"

Aminatu ta faɗa tana balbale khadija da harara,

cikin sanyi fateema tace,

"haba aminatu bai dace ba gaskiya abinda kikeyi,yakamata ace idan wani abu khadija tayi miki kisanar da ita bawai kiyi mata haka ba"

da tsabar fushinita aminatun tasake hayayyaƙowa,

"bazan sanarba fateema!inhar bazaki tahoba ni kinga tafiyata"

Ta faɗa tanayin gaba,

A wani mugun fusace khadija ta jawo aminatu baya tareda turata baya da ƙarfi tayi taga'taga zata faɗi Allah yasa tayi tsaye,

Cikin tsabar ɓacin rai da masifa ta fara magana,

"ke kin isa ki faɗamin kuma ki tafi ban mayar miki ba,wllhy ko haihuwarki ba'a yiba,kuma daki faɗi abinda nayimiki da karki faɗa uwar ubansu ɗaya!matsalarkice ke tashafa,sgashasha kawai,"

Tana yɨarasa maganarta ta balbalesu da harara gabaki ɗayansu tagi gaba,

Itama aminatun gaba tayi abinta dan kiwa tasan halin khadija,

A tsaye suka bar fateema sororo tana nazari kafin ta sauke gwauron numfashi ta nufi part ɗi aunty maimuna,

Tunawa da nasihar ammi yasa ta tsaya bakin ƙofa ta daidaita fuskarta daga fushi kafin tashiga cikin part ɗin da sallama,

Umma babba ce kaɗai a falon hakan yasa ta nufi kusa da ita ta zauna tareda ɗan jingina da jikinta kafin tace ,

"umma ina kwana"

Cikin so da ƙauna da tsantsar jin daɗin data rasa dalilin da idan taga khadijar take shiga cikinsa,tasake jawota jikinta sosai tareda cewa,

"lafiya yɨalau ɗiyata ya kika tashi"

"lafiya ƙalau ummanah"

Suna haka aunty zainab da aunty ruƙayya suka shigo daga ɗakinsu,

Suma zama sukayi aunty ruƙayya na tsokanar umma tanacewa,

"watakam umma ananiƙar ki tazo shine zaki watsaddamu ko"

Cikin fara'a umma take cewa' "eh kuma kubari taku uwar tazo"

"ai wllhy umma basai tazoba myma yaji zamuyi mukoma gurinta"

A haka dai akayita raha kafin khadijan ta tashi tafito,

Haushin aminatu ne yasa taƙi shiga part ɗinsu dan a tunani ta ko zata gamu da itane,

Da sallama tashiga part ɗon ammi,

Kamar yadda tayi tunani a falo ta sameta a zaune cikin shiga ta kamala,

Sidai kuma da ka kalli fudkarta zaka san tana cikin damuwa,

hakan yasa khadija saurin ƙarasawa kusa da ita tareda tambayarta,

"ammi lafiya naganki a haka"

"Lafiya ƙalau khadija me kika gani"

"ya zakice lafiya ammi bayan na ganki cikin damuwa"

a hankaki ta ɗan yayalo murmushi kafin tace,

"wllhy kinga wayar yayankuce naketa kira tun safe amma har yanzu najita shiru tana ring bai ɗagaba"

Har ga allah khafija ta zata yaya mamman ammi take nufi hakan yasa tace,

Kuma ai ɗazu da sassafe najishi yana yiwa hajjaju magana,to ammi ke ammi ina kike tunanin yaya mamman zao shiga?"

ta faɗa cikin damuwa,

Ammi cikin sake bayyanar da damuwa tace,

"nifa ba shiba"

"to ammi wa"

"Ok mamman ne kalai yayanku"

Ammin ta faɗa a ɗan tunzure,

Sai lokacin gane tashar da ammin ta nufa,

Kayy gsky ammi da ɗorawa kai take yanzu dama wancan gardin ne yasa hankalinta tashi haka?

lallai kuwa tanada aiki wama yasani ko a wani gidan karuwan ya kwana yasa yaƙi ɗaga wayar,

Da sauri ta furta,

"astagafirullah"

Tunowwa da hadiain ma'aiki SALALLAHU ALAIHI WASALLAM,

ɗan taɓe baki tayi kafin ta miƙe tana cewa ammi,

"naji kamar su fateena a gidan",

tunda ta fara abinta ammi tana kallonta har taɓe bakin datayi hakan yasa tana kai ƙarsgen maganarta ammi tace mata,

"khadija zo nan"

A hankali ta koma ta zauna kusada ammin,

Ammi tasoyiwa khadija faɗa saidai kuma taga kamar lamarin khadija da zayyad bayajin faɗa hakan yasa ta canza akalar faɗan nata zuwa nasiha,

a hankali ta jawo hannuwanta biyu ta riƙe tareda yɑ̈ura mata idanu ta fara magana,

"yanzu khadija abinda kikeyi yakamata,shin bbakisan zayyad ɗan uwanki bane,meyasa kike haka,ko sokike a ringa kallonki a marar tarbiyya mai faɗa da yayanta, shifa zayyad ba tsanarki yayi ba halayenkine bayaso kuma dakin bari zakiga kun daidaita yanayimiki kamar kowwa,

Koba komai zayyad ya ɗaukeni tamkar uwa ke maizaisa bazaki ɗaukesa yaya ba,"

sosai ammi tayiwa khadija nasiha kafin tace taje part ɗinsu tagani ko yana nan,

Hrar ga allah jikinta yayi sanyi da nasihar ammi amma ita wllhy batason haɗuwa da yaya zayyad ko kaɗan,sai dai bazata taɓa iya faɗawa ammi tsakaninta dashiba amma taci alwashi yaƙu da abinda takeyimata,

A sanyaye ta miɣe ta nufi ha yar fita,

Yau zayyad ya tashi da wani shegen zazzaɓi da mura wanda hakan yasa ya kasa fitowwa daga ɗakinsa dan gaskiya sosai yakejin zazzaɓin,

A takure yake cikin bargo yanata kyarma,sosai yake kyarmar dan hatta bargon jikinsa ya ɗauki ɗumi ga shi haƙoransa sai kaɗuwa suke,

Duk yadda yaso ya ɗaga hannunsa ya ɗauki wayarsa datake rurin neman taimako ya kasa duk kuwa da kiran dayakeji da ring daban daban amma yakasa ɗauka,

Gashi gabaki ɗaya ƙannensa ya haramta musu shigarmasa ɗaki barema wani yasan bashida lafiya,

MURAYE GIDA😆😉😆MASHI GARINMU

_____□□□□□□□□□ *DR ZAYYAD*

40&41

MALLAKAR

HAJARA MURAYE

(MRS AMINULLAH)

□□□□□□□□□

nakune *TEAM ZAYYAD ** *ina bada** *gaisuea*

_____tunda khadija ta taho taketa faman kumbura tana cika tana batsewa a haka har ta isa part ɗin yaya zayyad ɗin,

ta daɗe a bakin ƙofa tana shawara da zuciyarta kafin tayi ƙundum balar kutsa kanta cikin part ɗin,

A hankali ta gama ƙarewa babban falon kallo wanda gabaki ɗaya ya hargitsa shi sai kace wanda aka yi wasan tsere acikinsa,

Taɓe bakinta tayi tareda cewa,

"ƙazami kawai"

Da sauri ta ɗan dafe bakinta tareda waigawa gefe da gefe kafin tasaki bakinta tareda yin wani guntun tsaki,

Ganin baya falo yasa ka ta juya da nufin komawa ta faɗawa ammi baya nan,

Har ta fara tafiya sai kuma taɗan fara jiyo sautin nishi kamar na marar lafiya,

Hakan yasata saje kasa kunnenta dan tabbatarea,

Tabbas nishi takeji,to amma waye bashi da lafiya kuma ba'a saniba,

Da sauri ta nufi inda take jiyo sautin tareda ƙara miƙa kunnenta daidai ƙofar ɗakin yaya zayyad,

Tabbas a ɗakinne,but amma yaya zayyad bashi da lafiya shine bazai kira ya faɗa ba kuma ayita kiran wayarsa amma yaƙi ɗagawa,

cabbb ɗin gaskiya mugun halin yaya zayyad sai shi,

Yanzu dan tsabar mugun hali kana a hannun allah amma ciwonma dai ka nuna masa miskilanci,aikuwa zaka gasu dan wllhy inda kace haka zakayi to kana tareda wahala,

Tana kaiwa nan a tunaninta ta taɓe bakinta tareda yin hanyar waje abinta ba tareda ta damu da shiga taga a wanne hali yakeba,

koda ta koma part ɗinsu ta iske ammi a tsaye da waya a hannunta still tana sake kiran yaya zayyad ɗin,

Da sauri ammi tayo wajenta ganinta dawo, ko kafin tayi magana ma ammi ta tareta dacewa,

"baya nan ko khadija!innalillahi!wai ina zayyad ya shigane"

Saroro khadija tayi tana kallon ammi da zuea yanzu har hankalinta ya tashi,

Wai me hakan yake nufi kenan ammi tafison yaya zayyad akanta,

cabbbb aikuwa wllhy ba'a isa ba!tunda hakane kuwa wllhy bazata taɓa faɗawa ammi halinda yaya zayyad yake cikiba gwara ma ya mutu kowwa ya huta da baƙar azabarsa,

D sauri ta ɗan yaƙalo murmushi tareda cewa,

"Kayyy ammi ki nutsu mana ni wllhy har tsoro kike bani kin wani damu da shi amma shi dayake baidamu dakeba yama bar wayarsa a ɗaki kinata faman kira,shinefa dana ga kintashi hankalinki na ɗauki wayar tasa nakira yaya fu'ad nake

tambayarsa shine yacemin yanzu haka auna tareda yaya zayyad ɗin wayar ya manta a gida, shinefa ma yaya zayyad ɗin yace nacemiki ya manta wayarne amma kiyo haƙuri da wuri ya fita shiyyasa bai shigoba,"

Tunda ta fara maganar ammi ta tsareta da idanu gani alamun kamar batada gaskiya,sai da takai ƙarshen zancenta kafin ta fara yɗan kyafce ƙyafce,

"anya kuwa khadija?"

Gabanta ne yayi wani mummunan faɗuwa,amma dayake tana kan dokin mugunta ne yasa ta dakewa tareda cewa,

"wllhy Allah kuwa ammi da gaske nake"

"Shikenan"

" Ni bansaki rantsuwa ba"

Cewar ammin,

Wata nannauyar ajiyar zuciya khadija ta sauke tareda dafe ƙiji tace,

"waiii allah na godemaka"

Ai kuwa karaf a kunnen ammi,da sauri ta juyo tareda cewa,

"khadija!"

Cikin kiɗima da burcewa da in'ina tace,

"naaaaam ammi"

"menaji kince?!"

"Ammi hamdala fa nayi"

ta faɗa a shagwaɓe,

Sosai ammi ta kasa yadda da maganar lhadija hakan yasa tace,

"wuce kije ki ɗaukomin wayar yayannaku,"

Ƙuuuuuuuuuuuuu,

cikin khadijar yayi wani masifaffen kaɗawa aikuwa ba shiri tajingabanta yayi wani mummunan faɗuwa,

"Ammi in ɗauko wayar"

"yess hakanace!"

Ammi ta faɗa tareda tsare gida da tabbatarwa,

kamar wadda ƙwai ya fashewa haka ta fara tafiya,

A ranta tana,yau na shiga ukku shikenan naga takaina, a haka har ta fice daga falon,

A ƙofar falon ta tsayantana yan ƙyafce2,

"yanzu ya zanyi ni khadija,"

T ɗan ɗauki pan mintina kafin dabara ta faɗomata aikuwa da sauri tayi part ɗin hajiya ko waigowwa batayiba,

Sai da ta ganta a falon hajajju kafin ta dafe ƙirjinta tareda sauka wata ajiyar zuciya tace,

"Alhamdulillahi! nasamu na kuɓuta"

"Daga hannunwa"

taji muryar hajiya ta daki dodon kunnenta,

Da sauri ta ware idanunta dan harga allah bata san hajiya na falonba,

Ta tsorata sosai amma ganin hajiyarce yasa ta saki jikinta tareda labartawa hajiyar duk abinda ya faru,

Amma sai ta ɓoye mata cewar ta ji yaya zayyad ɗin ba lafiya, T dai cemata,

"wai ammi ce ta aikwni indubo mata yaya zayyad a ɗakinsa dan kawai ta kirashi bai ɗaga ba,kuma wllhy kindaisan halinshi sarai gajiya innashiga zai iya kasheni shinefa na lame sai da na ɗan jina kafin na dawo naɗan samu ƙarya nayimata dacewar na je sai wayarsa amma nakira yaya fu'ad yacemin suna tare,wai bata yadda ba saina ɗauko mata wayar, nikuma nayo nan,"

"dan allah hajiya kice ina firowwa kika kirani"

"A'a ni wllhy bazaki koyamin ƙaryaba kajimin ja'irar yarinya"

Da sauri khadija ta matso jikin hajiya tareda dafa cinyoyinta,

"haba hajjajuna ai wllhy nasan bazaki taɓa bari wani abu yasameni ba namasan zaki faɗa ko sweet heart"

"Hmmm yaudara dai ba wani abu ba hadiza kin iya ta"

A haka dai khadija ta lallaɓa hajjaju daga nan suka shiga wata hirar abinsu,

A ɓangaren ammi kuwa tunda khadija ta fita take tantama akan abinda khadijan ta faɗa sai dai kuma bata taɓa kama khadija da laifon ƙarya ba hakan yasata ɗan samu natsuwa da rashin ɗaga wayar zayyad ɗin,

Sai dai kuma gani shiru khadija bata dawoba yasa ta leyawa ɗakin da su ummy suke suna ta shan hira abinsu,

Ganin babu khadija yasa ammi cewa ummy taje part ɗin yayansu tagano mata ko lafiya ta aiki khadija amma shiru,

Ai tsalam aminatu ta tashi jin an ambaci part ɗin su yaya zayyad dakuma khadija,

ko kafin ummy ta ɓiƙe tuni tayi waje,

Hakan ba ƙaramin mamaki yabawa ummy da fateema harma da ammi ba,

Amma ganin ba fuskar magana a gurin ammin yasasu yin shiru tareda miƙewa dan cika umarnin ammin,

Tuni aminatu ta kama hanyar part ɗinau yaya zayyad dan ko kafin su ummy su fito hatma ta ɓacewa ganinsu,

Koda suka fito babu wanda ya tanka gameda abinda aminatun tayi har suka isa part ɗinsu yaya zayyad,

Da sauri suka ƙarasa cikin ɗakinnasa dan jin yadda aminatu ke fitarda sautin siririn kuka,

To suma ba ƙaramin tayar musu da hankali lamarin yaya zayyad ɗin yayiba dan gabaki ɗayansa ya faɗo daga kan gadonnasa yana kwance shaɓe,shame cikin amai,

Sosai lamarin zai baka mamaki ta yadda gabaki ɗaya ya fita daga hayyacinsa sai numfashin da yake fitarwa da ƙyar,

da gudu ummy da fateema suka fito hankali tashe suka nufi part ɗin ammi,

Koda suka ƙarasa ammin tana tsaye dai still da wayar a hannunta ya zuwa yanzu fa hankalinta yayi gagarumin tashi,

cikin tsabar kiɗima ummy takw cemata,

"ammi yaya zayyad!"

sosai gaban ammi yake faɗuwa da sauri tariƙe ummyn tareda girgizata,

"ummy meyasamu zayyad ɗun!"

Ammi ta faɗa cikin kiɗima,

daƙyar ummy ta iya daidaita kan ta kafin tace cikin haki da ƙaguwa,

Ammi yaya zayyad yanacan kwance cikin amai kamar marar galihu rai a hannun allah"

Ko kafin ta kai ƙarshema tuni ammi tayi hanyar part ɗin yaya zayyad ɗin aguje,

kamar wasu taɓaɓɓu haka suka sake kwasa fateema tayi part ɗin umma ummy kuma tayi part ɗin hajjaju.....ayi manage ba yawa

ALHERIN MUTANEN DAURA YƇAR MUTAN MIRAYE CEhaka suka gama ysare-tsaren sukafin merry ta tsinke wayar tareda yin wani ihu ta faɗa kan gado cikin wani irin shauƙi mai kamada anyimata wahayin godan aljanna,

A hankali ta tashi tana wani rangaji ta nufi windown dake ɗakin tareda saka hannunta dayaci uban bliching ta yaye labulen ɗakin gamida kutsa kanta jikin ƙarafan tana shaƙar tatacciyar ni'imtacciyar iskar gari,

Da wani salo tafara kaɗa idanunta tareda yin fito da bakinta cikim salon iya bariki da duniyanci,

ta jima a haka kafin ta saki windown tareda dawowa baya ta zauna akan kujera kafin ta ɗauki kwalbar syrup ɗin data saba kwankwaɗa,

Lallai tau tana cikin farinciki marar misali dalilin nasarar datake ji tana tattare da ita,

A hankali ta ɗaga laɓɓanta tareda furta kalmar,

"Zayyad nawane ni kaɗai bazan taɓa barin wata ta kusanceshiba,"

A haka dai tayita surutanta kafin ta ci gaba da bankar surup ɗinta,

A ɓangaren fareeda ma tana ajiye wayar murmushi tayi tareda furta,

"da sannu zan gama amfani dake merry na mallaki abinda nakeson mallaka kafin na watsadda ke,danna ci alwashin ko gate ɗin gidana bazaki raɓa ba saboda muddin dangin zayyad suka ganki bazasu taɓa amincewa zayyad shi ne ummul aba'isin lalata rayuwata ba"

Itama dai a haka taciga ba da yƙan surutanta lafin ta ɗauko emblope ta fara shirya hotunansu itada zayyad,

_____tinda suka fito khadija take raɓe-raɓen bin bayan hajajju har suka isabakin part ɗin ammi,

jim hajiya nata tafiya kamar ba'a binta yasata tsayawa tare da juyawa,

Aikuwa a baya taga khadija ta toge ta wani manne a jikin bango,

Ganin haka yasa hajjaju cewa,

"aa lafiya naga kin wani maƙale a baya"

Amma kamar ba da khadija take magana ba,

"wllhy kika sake saina komawa ta"

Da sauri khadijan ta matso tareda kama hannun hajiya idanunta taf da hawaye tace,

"dan allah hajiya karki bari ammi ta dakeni wllhy nayi nadamar abinda na aikata"

"Hmm hadiza kenan ashe kinajin tsoro kuma kika aikata"

"haba hajiya ba kinyimin wa'azi ba kuma ainace insha allahu bazan sakeba"

"To shikenan muje ai kindai san mudfin muna tare babu abinda zatayi miki"

Da haka khadija tayi shahadar bin hajajju suka kutsa kai cikim falon ammin,

tana cikin falon kuwa akan dining tana haɗa kayan dazata kaiwa dr zayyad ɗin,

Jin sallamar hajiya yasata ajiyewa tayo falon tana amsa sallamar hajiyar,

kamar yadda tayi tunani haka tasamu watakam ganin hajiya da khadija,

Hakan yasakata ɗan haɗe fuska ko kallon khadijar batayiba tacewa hajiya,

"hajiya akwai abinda kike buƙata ne"

Ɗan murmushi hajiya tayi tareda cewa,

"hmmm babu abinda nake buƙata uwar zaidu afuwa dai mukazo nema"

Yanayin yadda hajajjun tayi magana neyaɗan saka ammi sakin fuskarta tareda ɗan sunkuyar da kanta ƙasa kafin ta fara magana,

"amma hajiya sai nake ganin kamar ƙyale khadija da akeyi ba'a hukuntata shine yakesakata aikata duk abubuwan datake wani lokacin"

"Nasani amma dai to dan allah a taimaka daga wannan insha allahu bazata sake ba"

"Hmmmm hajiya kenan kullum ace daga wannan,yanzu girman laipin da khadija tayi baici ace kin ƙyaleta an hukuntataba,wllhy da ace zayyad ya mutu to da khadija nada haƙƙi rai akanta,wai wannan wacce orin tsanace yarinyar nan take

nunawa bawan allah nan ne,haba hajiya ace babu wanda zaka nunawa tsana sai ɗan uwanka,wllhy basau ɗaya ba bakuma sau biyu ba gata nan a gabanta nasha nuna mata irin abinda takeyi bashida amfani amma har yau ta gagara fahimta"

sosai jikin hajiya yayi sanyi da maganganun ammi sai dai kuma duk da haka tana kan bakanta na bawa ammin haƙuri hakan yasa itama tacigaba da cewa,

"Nasan da haka kuma nasan duk abinda kike faɗa akan gaskiyane sai dai fa kisani nunawa hadiza ɓacin rai bashi zaisa zucoyarta sauyawa ba,"

Sai da ta ɗan ƙara tsahirtawa kafin ta dubi khadija tace,

"Hadiza wuce gurin maimuna kafin innemeki,"

Da sauri khadija ta nufi part ɗin aunty maimuna wadda itama yazuwa yanzu ummy ta sanar da ita gabaki ɗayan abinda khadijan ta aikatawa yaya zayyad ɗin,

hajiya ce ta kalli ammi da tsantsar fahimta kafin ta cigaba da magana,

"haƙiƙa naso ace nasamu gabaki ɗaya surikkaina halinku ɗaya sai dai kuma kash!

tun ba'aje ko inaba nafara samun nara gurbi da kuma tangarɗa wanda bazan taɓa lamuntar hakanba,

ALLAH yasani gabaki ɗayanku daidai kuke a guna sai dai kuma ita kyatatawa da biyayya kansa kaji wani sama da wani a ranka,

Haƙiƙa nasan ina tauyeki akan abubuwa dadama musamman akan hadiza,

Sai dai kuma inaso ki fahimta ni inaji ajikina cewar akwai wani ɓoyayyen lamari da hukunci zartacce akan hadiza da zaidu,

Dan haka kisani bawai da ƙarfi zaki iya cire ƙiyayyar zaidu daga ziciyar hadiza ba,aa zai fi kyau ki ɗauki wasu dabaru a matsayinki na uwa wanda zaki tisa wa hadiza ƙaunar zaidu ki kuma yi nasarar cire ƙiyayyarsa azuciyarta,

Muddin kikayi haka ni kika taimaka da kuma wani ɓoyayyen sirri na wasu zukata masu tarin yawa"

Tunda hajiya ta fara magana ammi take saurarenta tareda yiwa maganarta kyakkyawar fahimta dakuma ɗaurata a mizani na tunani da hankali,

Sosai ta karɓi maganar hajiya tareda yimata mazauni a gurbin tunaninta wanda hakan yasakata yiwa hajiya godiya tareda nunamata insha allahu abin yariga ya wuce,

Itama hajiya sosai taji daɗi tareda sake bawa ammi yɷan shawarwari kafin tayi mata sallama ta nufi part ɗinta,

Tunda hajiya tafita ammi ta koma ta zauna tashiga tunanin maganganun hajajju tabbas komai na babba yafi na yaro haƙiƙa ita kam tafi khadija tinani amma itama hajiya tafita tunani da hangen nesa,

Sannnan kuma muddon abinda hajiya ta faɗa tayimasa kyakkyawar fassara dakuma fahimta to tabbas a kwai ƙura dankuwa ƙuru ƙuru ta hango wutar soyayya dakuɓa ƙaunar zayyad a idanun aminatu da mahaifiyarta dake muradin da goyon bayan yaɗarta,

Any way dai aminatu da khadija harma da zayyad yaɗayantane dan haka bazata taɓa son ganin an ɓata wa kowwa ba dan haka zata dage da addu'ar Allah ya zaɓa musu mafi alkairi baki ɗayansu,

Amma dolene zata dagewa khadoja kamar yadda hajiya ta faɗa ta hanyar ƙara jawota a jiki da nuna mata illar abinda take aikatawa uwa uba zata dage mata da addu'a sanin kowace mama babba akan burin datasa a gaba,

Da wannan tunanin daia ammi ta tashi tacigaba da aikinta ganin lokacin tashin zayyad ya ƙarato,

Tunda khadija tashiga parta ɗin aunty maimuna suka ƙule a ɗaki tana nuna mata kuskuren da ta aikata da kuma illolin ƙiyayya ga ɗan uwa,

To dayake dai ance mai laya kiyayi mai zamani tuni auntu maimuna ta samu kan khadija a hankali take cusamata wasu ra'ayiyyika cikin tsabagen wayewa da hikima,

A haka dai suka ci gaba da hira har aunty maimuna ta shawo kan khadija akan zata je tabawa zayyad ɗin haƙuri akan abinda ta aikata kodan ammi ma,

Bata barta ba har sai da ta yadda suka shiga khitchen dan haɗawa marar lafiya delicious,

tun khadija na ɗari ɗari harta saki jikinta dayake aunty maimuna ma gwanace haka suka ɓata lokaci wajen yimasa farfesun kayan ciki dayaji kayan yaji da attaruhukafin akayimasa yan snacks da shayi mai kayan ƙamshi,

Sai da aka kusa gama kafin aunty maimuna ta cewa khadija ta wuce part ɗin hajajju ta gyara jikinta kasancewar sun shiga khitchen kafin su wuce part ɗin yaya zayyad,

Haka kuwa akayi part ɗin hajajjun ta wuce sai dai batayi mamakin ganim babu hajjaju a part ɗinba ta tabbatar tana part ɗin yaya zayyad,

Ba tareda ɓata lokaci ba ta yi wanka tareda turare jikinta kafin ta shirya jikinta cikin wata A sharp ta less bluee mai adon fulawoyon sky blue tareda taje gashinta ta ɗaureshi a can ƙasan ƙeya kafin tayimasa ɗaurin ture kaga tsiya,

Gsky khadija kyakkyawa ce ta ajin ƙarshe dan shigar ba ƙaramin karɓarta tayiba,

plate shoes ta saka baƙi tareda maƙala fashion ɗan kunne baƙi mai ɗan yalwar girma,

ba tareda ɓata lokaci ba ta fito dan a ƙofar part ɗin aunty maimunan ma ta ganta,

Tunda ta taho aunty maimuna ke ƙissiɓa abubuwa dayawa a zuciyarta akan khadijar gaskiya khadija kyakkyawace dan haka ma babu da wanda ta dace face zayyad,

Da murmushi ta tareta tareda koɗa iron kyanta kafin suka kama hanya,

Har suka isa aunty maimuna na jaddadawa lhadija akan tabawa yaya zayyad haƙurin abindatayimasa,

A falon auka sami kusan rabin gidan amma banda umma babba kasancewarta mace mai kara da kawadda kai,

Da sallama suka shiga wanda dayawa daga cikin mutanen falon sun amsa amma banda mama babba da aminatu,

Da suke aikawa khadijar dawata muguwar harara sosai kishin kyawun khadijar ke takurawa mama babba,

A hankali khadija ta gaisheda mutanen falon sai dai kuma kowa ya kula da otin amsawar da maman tayi,

Ganin batayiwa zayyad maganaba yasa ammi bamka mata wata uwar harara wadda saida yan hanjinta sukayi zallo,

Babu shiri wani siririn hawaye yazubomata,

Auntu maimuna gamin khadija zata ɓata musu shiri akan huɗubar sirrin datayimata yasata ɗan mintsinar khadijar,

A hankali kamar wadda ƙwai ya fashewa tamiƙe tareda komawa kusada yaya zayyad ɗin da tunda tashigo yake ƙaremata kallo ta ƙasan idanu tareda addabarsa da fitinannen ƙamshinta yayi,

Jin ta akusadashi ba ƙaramin tsinkewa zuciyarsa tayiba tareda karɓar dukan take masa wanda yake daidai da ƙariwar ciwonsa,

A hankali ta ɗauki hannunta ta ɗora akan ƙafafunsa wanda yakasance daga cikin huɗubar aunty maimuna,

Cikin airoroyar shagwaɓaɓɓiyar muryarta mai kamada anyi gudun tsere tace,

"pls kayi haƙuri yaya zayyad"

Da sauri ya rumtse idanunsa dalilin wani tsimkewa da jininsa yayi gabaki ɗaya ji yake kamar ya rumgumota saboda jin wani abu dayake addabar zuciyarsa,

A hankali hawayenta suka sauka akan ƙafarsa wanda ya kasance tamkar saukar mashi a ƙahon zuciyarsa dan kuwa jin danshin ruwa a ƙafarsa ya tabbatar masa da hawaye take,

Kenan akwai abinda tayi masa wanda baisaniba,

Koma dai menene shi kansa ransa fansa ne akan ƙannensa musamman ma ita dayake jinta har cikin ƙoƙon zuciyarsa,

A hankali ya kai hannunsa saman kanta yasake jawo kanta zuwa kan dantsen ƙafarsa yana bubbuga kannata alamun sorry batareda yayi magana ba,

ɗif!!!

Wuta ta ɗaukewa gabaki ɗaya zukatan dake falon wanda dayawansu hamdala sukeyi akan daidaituwar zukatan biyu dasuka fara gani yayinda wasu zukatan tsayawarsu take daidai da barazanar tsinkewar ruhim na har abada,

Musamman aminatu da tun ɗazu take ɗauke wasu zafafan ƙwalla dasuka ɓalle wa fuskarta tamkar famfo,

Kyasss!!!

Hasken camera ya fallasa asirin ɗaukar da aunty maimuna'aunty ruƙayya da aunty zainab sukeyi,

Wanda ya saukar da wani rugugin azaba da raɗaɗi a zuciyar aminatu,

Da gudu ta miƙe tayi waje wanda har ga allah dayawan mutanen gurin basu wani damu da hakan ba wasuma basu ganiba saboda yadda hankalinsu yakoma kan su zayyad,

Hajajju ma a hankali ta ɗauke wasu ƙwallan farinciki ganin burinta naneman cika tarefa yiwa allah godiya,

haskaen camera ne ya maido yaya zayyad duniyar tumaninsa kafin yayi nasarar saɓule hannunsa,

a hankali dai itama mama babba tabi yarta dan gaskiya tata zuciyar zata iya bugawa,

To itama dai ammi ganin su aunty maimuna nason canza tashar datake ne yasakata sulalewa ita da umma da mama ƙarama kafin aka barsu suda hajajjau,

a ahnkali yaya zayyad ya ɗaga kansa tareda kallon aunty maimuna yace,

"Aunty me kika kawomin ne"

dariya ta ɗanyi tareda nunamasa khadijan ta wutsiyar idamu batareda gabaki ɗaya yʼan guron sun fahimta ba,

So shima dayake ɗan duniyane ya luma fahimceta sai yayi murmushi tareda basarwa yace,

"wai ko bano kika kawowaba"

"kodai banina kawoba dan inda ninakawo ma ai da tuni na miƙo maka dan haka wanda yakawo maka da kansa zai baka"

A ransa yace,

kai wannan matar yʼar tada ɓalli ce wallahy,

kamar kuwa tasan me yace sai kuwa ta ɗanyi murmuahi tareda cewa,

"ai ni haka nake kamar ciwon ajali imnakama sai na kawas"

"Hmmm ai kinma fishi"

Hajiya dai ganin tana gyangyaɗi yasakatayin part ɗinta dankuwa ba lokacin bacci bane dan yamma tayi sosai,

yadda aunty maimuna ke kallon khadijane yasakata tashi a hankali taredalallai ta tafka babban kuskuren barin ammi ta shigo gidan har take nemanzame mata ƙarfen ƙafa,

inkuwa har ammin tafara neman kawomata cikas ko tsaiko a kan buƙatar ta to yazama dole ta ɗaura ɗamarar kawaddda ita daga gidan.kai ita akan buƙatarta fa babu abinda bazata iyayiba sannan kuma babu wanda bazata kara dashi ba ciki kuwa har da hajjajun data haifi uban zayyad takuma haifi uban aminatu take kuma a matsayin uwar mijinta,

tirƙashi!!!

a haka mamatacigaba da yʼan tunane2 Har zuwan yaya fu'ad,

Bayan zuwan yaya fu'ad ɗinne ya umurcesu da fita dan duba jikin yaya zayyad ɗin,

To haka dai suma gabaki ɗayan iyayen suka fita harda hajjaju,

Kowa ya nufi parta ɗinsa da alhinin jikin yaya zayyad ɗin musamman ammi da gabaki ɗaya hankalinta da tunaninta suke akan zayyad ɗin,

Sosai yaya fu'ad ya shiga cikin aikin binciken jikin yaya zayyad ɗin sai dai kuma kamar yadda yayi tunani haka yasamu watakam dai matsalar datake daɓun zayyad ɗin ada yanzuma itace,

Sai dai fa yanzu sosai ciwonnasa yayi girma yakuma canza salo duba da daɗewar ciwonnasa dakuma yadda yanzu mataalar take ƙara ta'azzara dubada yadda ƙarfin sha'awar zayyad ɗin ke ƙara ƙarfi,

Kawo yanzu shi kansa fu'ad ɗin ya fara tsorata da lamarin zayyad,

Taya za'ace mutum ya karanta sannan kuma yasan matsalar datake taredashi babbar matsalace sannan kuma yasan bata da wani magani dayawuce aure amma yatsaya yana ɓata lokacinsa ta hanyar ahan ƙwayoyin dayasan koda sun masa magani baaifi na yɾan awannni ba kuma ciwon zai sake dawowz fiye dana da?

Gsky yazama dole yayi wani abu domin ceton lafiyar abokinsa tundashi bazai taɓa ɗaukar wani mataki ba,

ba sau ɗaya ba yasha bawa zayyad ɗin shawarar tin aure tunda yasan halin abokinsa sarai bazai taɓa iyayin sex da wata wadda ba matarsa ba,

Haka dai fu'ad yayita yɾan tinane tinane amma yakasa samun mafitar abin sai dai yabari har zayyad ɗin yasamu lafiya kafin su tattauna sosai akan lamarin,

Ganin yana buƙatar hutu yasa ya haɗa masa da allurar bacci kafin yasaka masa drip,

Ya jima a zaune agurin kafin ya miƙe zuwa part ɗin ammi kasancewarsa tamkar ɗan gida a gidansu zayyad ɗin,

Itama ammin daga part ɗin zayyad part ɗinta ta wuce dan sama masa abinda zai ɗanci dan ta tabbatar baici komai ba sannan ga aman dayayi tasan yana buƙatar abinci,

A ƙasan ranta kuwa sosai lamarin khadijar ya ƙonamata rai wanda bata taɓa tunanin ƙiyayyar da khadijar takeyiwa zayyad takai har taganshi a halin dayake ciki sannan takuma yi biris dashi saboda tsabar ƙiyayyar datake masa,

ita kanta ta tabbatar da zayyad ɗinne yaga khadija a cikin irin wannan halin bazai taɓa barintaba,

A haka ammi ta cigaba da saƙe saƙe dakuma alwashin hukunta khadijar akan abinda tayi,

tana khitchen yaya fu'ad yayi sallama ganinta a khitchen yasashi nufar babban falon dan jiran ammi,

Bata wani jimaba itama ta shigo falonbayansake gaisawa dasukayi ta tambayeshi jikin zayyad ɗin da tambayar abinda yake damunsa,

Ya so faɗamata amma sai yayi runanin zayyad bazai taɓa jin daɗin abinda zai yinba,

Koda ace ma zai faɗa ɗin to bai dace ya faɗawa ammi ba yafi cancanta ya faɗawa wani daga cikin iyayensa maza,

Wannan tunanin dayayine yasakashi furzadda ɗan zazzafan iska kafin yace,

"ammi zazzaɓine kawai amma nama sakamasa ruwa tareda allurai nasan insha allahu idan ya tashi zai ɗan warware,sai dai kuma zai ɗan samu hutun kwana biyu saboda yanayin jikinsa, sannan kuma inya tashi yasamu yaɗanci wani abu ko ba yawa,"

"Ok badamuwa allah ya baahi lafiya insha allahu idanyatashi ɗin zai ɗan samu yaci wani abin"

"ba damuwa ammi,nima bara na ɗanje kafin yatashi insha allahu zan dawo"

"OK badamuwa fu'ad sai kadawo ɗin"

Bayan fitarsane ammi ta aiki ummy ta kiramata khadija a part hajiya,

_____tunda mama babba ta dawo part ɗin ta takasa zaune ta kasa tsaye ta rasa ta hanyar da zata ɓullowa lamarin duk hanyar data ƙulla sai taga bazata taɓa ɓille mata ba,

A haka dai tacigaba da yɨan saƙe saƙe kafin daga bisani ta ɗauko wayarta tareda latsawa ta fara neman wata nmb,

Har wayar ta kusa tsinkewa kafin aka ɗaga

tun kafin tayi magana ma daga ɗayan ɓangaren aka sheƙe da wata dariyar duniyanci tareda cewa,

"Dama nace ina nan zaune zaki neme ni hajiyata kuma gaki"

Wata ajiyar zuciya mai sanyi mama ta sauke kafin tace,

"look hajiya ruƙayya dan allah kiyi haƙuri kimance da dukkan abinda ya faru ellhyina cikin yanayin damuwa"

Daga ɗayan ɓangaren cikin yanayi na kwantar da hankali aka cigaba,

Haba ƙawata aini dama ban wani ƙullacekiba nadai barkine kawai kiganeda kanki cewar gidanku zumane dan haka dole saida wuta sannan kuma duk abinda

nake faɗa miki ada nasone ki zama shugaba a gidan ma'ana sai abinda kika ce amma kika ƙi gashinan yanzu tun ba'aje ko inaba,"

Da sauri mama babba ta katse ƙawarta hajiya ruƙayya dacewa,

"wllhy ƙawata ima cikin matsala sosai musamman nakeso mu haɗu muyi magana inasone kibani shawara"

"shikenan ƙawata amma fa kisani bazan zo gidankiba dan banmanta tsanar da wannan uwar mijin taki tayimin ba dan haka inkinshirya kya zo gidana"

"Shikenan ba damuwa hajiya ruƙayya nagode"

"karki damu ƙawata sai nazo"

Da haka suka tsinke wayar mama babba natuna irin duniyanci da makirci na tsohuwar aminiyar tata wato hajiya ruƙayya"

A ɓangaren hajiya kuwa tunda ta koma ta rufe khadija da faɗa akan abinda tayi kafin daga bisani ta shiga lallaɓa khadijar da nunamata abinda takeyi ɗin ba abune mai kyau ba da nunamata zayyad fa ɗan uwantane bai dace tana nuna masa hakanba,

Kamar wata ta allah haka khafija ta nutsu tana sauraren hajiya daabindatake faɗa mata akanhalayen kirkin zayyadɗin,

Sai dai fa kwata kwata babu abinda ke shiga kan khadija acikin maganganun hajiya na zayyad ɗin kawai dai tana saurarene dan kar hajiya tace ta rainata,

A haka ummy tayi sallama ta samu guri ta zauna kafin tace,

"khadija kije ammi na kiranki"

tunda ummy tashigo gaban khadija ke faɗuwa,

Hakan yasa tanajin an ambaci ammi cikinta yayi wani mummunan kaɗawa,

Ai ba shiri ta kwasa da gudu zuwa banɗaki gabaki ɗayansu binta sukayi da kallo cikin mamakin tsoron da syka gani a tattare da ita,

Lallai yau kuwa khadija ba ƙaramin saɓawa ammi tayiba,

Daƙyar ta fito gabaki ɗaya gwiwoyinta sunyi sanyi sai data ɗan tsugunna a bakin ƙofar banɗakin kafin ta taso tana goge ƙwallab idanunta,

A gaban hajiya ta tsugunna kamar mai neman gafara tareda ɗora hannuwanta bisan cinyarta ta fara magana tana hawaye,

"hajiya! kiyiwa allah dan annabi da al'qur'ani dan darajar tsohon mijinki dayake ƙasa ki rakani gurin ammi kibata haƙuri wllhy yau Innaje ni ɗaya kasheni zatayi,

ummy datake zaune tanakallonsu jitayi gaakiya idan tacogaba da riƙe dariyarta zata iya mutuwa hakan yasa tasaki bakinta tareda sheƙewa da dariya,

Ko hajiya da akewa magiyar kasa daurewa tayi saida ta dara dan gaskiya ba ƙaramar dariya khadijan ta bata ba,

dama haka khadika takeda tsoro haka?cabb,

Duk dariyar da suke bai wani dametaba inda abinda yake damunta a yanzu bai wuce yadda zasu ƙare da ammi ba,

Ganin bata tashiba yasa ummy cewa,

"wai kodai inje incemata bazakizoba?"

A fusace ta juyo tareda cewa,

"kutumar....."

"Kai!kai!!kai!!!"

hajiya ce ta tareta da sauri tareda cewa,

"wllhy kika ƙarasa khadija bazaniba"

Ai da sauri itama khadijar tace,

"wllhy hajiya bazan ƙarasaba yi haƙuri,dan allah ummy kiyi haƙuri"

Sosai dariya take sake neman ƙwacewa ummy hakan yasa tayi saurin ficewa daga ɗakin kafin daƙyar hajiya ta yadda zata raka khadija part ɗin ammin,

WAI INA LABARIN MERRY DA FAREEDA

_____to har yanzu dai fareeda na kinyar ciwon da khadija ta jimata a ta ɗayan ɓangaren kuwa tana tunanin bin shawarar ƙawarta merry kawai zata yadda tasaka hotunan a emblope ta bawa wani ya kai gidansu zayyaddan hakanne kawai zai saka su su yanke hukuncin aurawa zayyad ita dan a yadda merry ta faɗa mata a yadda mahaifin zayyad yake da adalci muddin yaga videos ɗinnan dolene zai tirsasa wa zayyad aurenta dan zata ɗaura alhakin ɓata tarbiyyarta akan zayyadɗin dan har ga allah bazata taɓa iya rayuwa babu shiba ta gwammaci ko wacce wahala a gidan zayyad ɗin data rayu bataredashiba,

Wannan hukuncin data yankene yasakata neman layin ƙawartata,

Bugu biyu merry ta ɗaga dan kuwa itama a nata ɓangaren tana zaunene tana tunaninta hanyar dazata raba zayyad da fareeda ko ta wacce hanya ma koda kuwa zatabi ta ƙarfin tsiya kai itafa a wannan karon ma zata iya nuna fareeda manufarta kai tsaye muddin bata yadda an bada hotunan nan ba,

to ganin kiran fareedar ne yasa merry saurin ɗagawa tareda nunamata damuwa akan jikinta,

A ɗayan ɓangaren fareeda tafara magana,

"ƙawata dama akan maganar zayyad ne yanzu kwata-kwata ma ya daina ɗaga kirana tun jiya hakan yasa na yanke shawarar kawai zamu shirya ne muje mukai wannan saƙonda kanmu,

Kamar anzuba merry ruwan rahama haka taji wanisanyi na ziyartar ruhinta,

Da wani salon duniyanci ta kaɗa idanunta tareda sauke kan wayartayi wani fito irinna yʻan-yʻan bariki kafin ta maida wayar kunnenta,

Cikin nuna halin ko inkula da zance tacemata,

"to ƙawata yadda kika gani sai ki fitar da lokaci sai muje mukai, amma fa zamu tsaya nesa ne da gidan sai mubawa yaro yakai"

" Sannan kuma zai fi kyau ki fitar mana da lokacin da gabaki ɗaya yʻan godan sunanan musamman iyayensu maza"qDate: Jul 30, 2022

Subject: DR zayyad 42&43

Har baccivya fara dan daukar hajiya da khadija, da ummy ta shigo part din Wanda hakan yasa su firgita suka tashibda sauri,

Cikin kidima da rudewa ummy ta fara korawa hajiya bayanin halinda yaya zayyad din gudu ciki,

Ko kafin ummyn ta kai karshema tuni hajiya ta rabata ta fice hankali a tashe,

Ganin hakannema yasa ummy ta bi bayan hajiyar itama hankalinta a tashe,

A tsaye suka bar khadija a sake da baki tana tunanin mafita,

Ba kalar shawarar da batayi da zuciyarka ba kafin daga karshe taja matasan kafafunta ta nufi dakinta,

A can part din yaya zayyad kuwa a rude ammi ta isa part din,

Ba karamin sakw tashi hankalinta yayi ba ganin halinda zayyad yake ciki,

Da sauri ta karasa gareshi tareda tallafoshi ta samu ta maidashi saman gadon kafin ta fara aikin gyara gurin daya bata da amai,

Tana tsaka da aikin gyara gurinne hajiya da su ummy suka karaso sosai itama hajiya tashiga damuwar ganin jikin yaya zayyad din,

Gefen gadon dayake hajiyar ta zauna tareda kai hannunta ta dafa jikinsa,

Sosai har yanzu zazzabin yake jikinsa cikin tausaya wa hajiya tace,

"Sannu zaidu! Allah ya bada lafiya ubangij yasa kaffarar jikine"

Bai iya amsamata ba saima sake dukunkune kansa cikin bargon dayayi,

Ana hakane su umma karama da aunty zainab da aunty rukayya suka shigo,

Sai dai sanin halin zayyad din akan wannan taron dasukayimasane yasa ammi yi wa yaran magana ceqar gabaki dayansu su koma cikin gida,

Haka kuwa akayi kowwa ya tashi amma banda aminatu da take zaune tundazu tana faman kuka,

Ganin hakan yasa hajjaju yimata tsawa,

"Watakam ke bazaki tashi ba kenan gaki isassa kowa ya fita amma ke kintsaya kina kukan munafurci, kokuwa ancemiki zqidun mutuwa zaiyi!?! Ko su sauran ba yan uwansa bane ke kikafi kowa sonshi? "

Kamar bazata tashiba kuma sai ta tashi tana tura baki ta nufi hanyar fita,

Da kallo hajiya ta buta kafin tace,

"Asssha wllhy amina kam kinyi asarar halin munafurcin kinnan,mtsss" taja tsaki tareda sake maida kallonta kan zayyad dayake kwance,

Ko sallama babu mama babba ta banko a firgice ta shigo part din kai tsaye gaban zayyad din ta nufa ba tareda tayiwa kowwa maganaba,

Da azama takai hannunta tana kokarin yaye bargonda zayyad din ya lulluva dashi,

Cikin sauri hajiya dake kokarin yiwa zayyad din magana ta mika hannunta tareda yin azqmar kama hannun Mamar,

Da sauri Mamar ta dago kanta a fusace,

Sai dai kuma ganin fuskar hajiya yasata yin sarander gabaki daya jikinta ya mutu,

Ta dan jima a haka kafin a hankali ta janye hannunta tareda yin baya ta zauna akan kujera,

Daganan babu Wanda yasake magana sai ammi datake faman gyara guri tagama tasaka turare kafin ta dauki wayar Dr zayyad din yafara neman nmbr abokinsa,

Tunda mama babba ta zauna babu abinda takeyi face aikawa da ammi wata uwar harara a fakaice,

Itafa ba karamin bata mata rai ammin nan takeyiba,sai yanzu ma take datasanin barin ammin tashigo gidan har ta zauna take neman nuna mata isa da takama,lallai dolene tasan abinyi tun kafin lokaci ya kuremata,

AYIMIN AFUWA WANNAN MA KOKARI NAYI SABODA MATSALAR WAYA DANA SAMU, NA TUNA DAKUNE KAWAI DAN KUNA RAINA,INA KAUNARKU NA HAR ABADA MY FANS,

YAR MUTAN MURAYE CE

Shared using https://www.writediary.com/getappyadda aunty maimuna ke kallon khadijanne yasakata tashi a hankali kamar wadda ƙwai ya fashewa ta nufi inda suka ajiye food flaks ɗin,

ƙaramin kofin ta ɗauka tafara tsiyaya black tea aciki kafin ta ɗauki plate ta buɗe flask ɗin farfesun kayan cikin,

aikuwa dandanan ƙamshi ya buɗe gabaki ɗayan illahirin falon,

sosai shima yayi maraba da ƙamshin tunkafin ta kawo masa,

zubawa ta fara yi cikin saiɓi take yi komai kamar mai tsoron yin laifi ko mai koya,

yadda take saraffa hannunta ne ya shagaltar dashi da kallonta har baisan sadda aunty maimuna tayiwa su zainab alama dasu tashiba,

bai lura da fitarsu gabaki ɗaya daga ɗakin ba sai da tagama zuba masa zata miƙe kafin yayi azamar ɗauke idanunsa daga kanta,

wayam! yaga ɗakin babu kowa sai dai bai damuba dan baisan uzurin su kuma ma ko ba komai shi hakan yayi masa,

kamar mai koyon tafiya ya ƙaraso gabansa tareda dire plate da cup ɗin a hankali lafin ta miƙe da nufi fita,

kawai jin tausasan hannunsa tayi cikinnata wanda hakan yasa ta sauke wata ajiyar zuciya batare da ta shirya ba tareda lumshe zara zaran gashin idanunta,

Jin shiru bai saketa ba bai kuma yimata magana ba hakan yasakata juyowwa da nufin yimasa magana,

Kawai tsintar idanunta tayi cikin nasa wanda hakan yasaka jijiyoyin jikinta daina aiki,

Bazata taɓa iya jurewa kallon cikin idanunsa ba hakan yasaka tayin azamar zare nata idanun daga cikin nasa,

"sit down"

Haka kawai taji ya furta wanda har ga Allah da ace bata kusa dashi sosai bazata taɓa jin abinda yace ba,

Bata wani musa ba ta zauna a kusa da ƙafafunsa tareda zurawa yatsun ƙagarta idanu tana wasa da su

Shima cup ɗin shayin ya ɗauka ya fara kurɓa batareda yasake yin magana ba,

sosai yake jin daɗin shayinhar cikin ransa hakan yasa baimasan ya shanye ba,

sai da yaji babu komai a cup ɗin kafin ya ajiye tareda jawo plate ɗin farfesun,

Shima dai yayi masa daɗi hakan yasa yaci sosai har sai da yaji cikinsa ya cika sosai kafin ya ture tareda kai dubansa gareta,

"zan wanke hannu da baki"

Kawai jin maganar tayi ta doki kunnenta,

Ita fa har ga Allah ta fara gajiya daga kuma tayi laifi kuma ta bada haƙuri dan dai kar ace bata da kunya fa yasa duk abinda akace tayi takeyi amma kuma sai mutum yayita wani ikon banza da wofi yana gadara tsabar miskilanci da gadara da muguwar baƙar ƙazantar tsiya ruwan wanke hannunma sai ankawowa mutum kan gado,

wllhy bazata iya ba,

haka tayi biros dashi kamar bata ki me yace ba,

ya kusan minti biyar a haka kafin yasake maimaita mata a ɗan harzuƙe

"nace miki zan wanke hannu da baki ko"

Sai da ta ɗan kumburo baki kafin ta tashi,

Shima ɗan tsaki yayi a ransa kafin yace,

"yarinya daga an sakarmiki rai sai raini da raahin mutunci"

Bayi tashiga har ta ɗebo ruwan a bokiti kuma ko me ta tuna oho,

Da sauri ta koma ta juye ruwan cikin masai tareda kunna hot water ta tara bokitin kafon ta ɗauko tana murmushi ta nufi gurinsa,

tana zuwa ta ajiye a gabansa tarefa cewa yaya gashi,

kamar wata ta Allah,

haka ya ambata a ransa tareda ɗan kallonta ta wutsiyar idanu,

Gani tana murmushi baisa ya kawo komai a ransa ba da dukkan comfidence ɗinsa ya tsoma hannunsa a bokitin da niyyar wanke hannunsa,

sai dai kuma yana tsoma yaji wani zafi ya zoyarci hannun nasa aikuwa bashiri yayo saurin cire hannunsa yana yarfawa dan gaskiya yaji zafi sosai

yanayin yadda yake yarfe hannuwa da yadda ya kyaɓe fuska yasaka ta kasa riƙe fariyarta aikuwa ta kwashe dariya,

Tun tanayi daga tsaye har takai da duƙawa ta dafe cikinta tana ta dariya,

Tunda ta fara dariyar ya shagala da kallonta gabaki ɗaya ma ya manta da zafin da hannunsa yakeyimasa dan a zahirin gaskiya ta tafi da imaninsa,

jin shiru yasakata tsagaitawa da dariyar tareda ɗaga kanta,

da sauri ta miƙe tareda tsayadda dariyarta,

cikin in ina ta fara magana,

"dan Allah yaya zayyad kayi haƙuri"

sauke ajiyar zuciya yayi kafin yasamu guri ya zauna a gefen gado gami da miƙa mata hannun,

da mamaki tabishi da kallo kafin taji yace,

"oya kiyita hura iska wa hannun nan da bakinki har sai ankira sallar magrib"

"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un"

khadija ta furta ganin datayi a jikin agogon dake manne a bangon saura kusan minti arba'in a kira sallah,

buɗe baki tayi da niyyar bashi haƙuri ya katseta,

"wllhy muddin kikayi magana anan zamuyi magrib da issha nidake"

Ba shiri kuwa taja bakinta ta rufe,sai dai kuma da gani ba alkhairi take saƙawa ranta ba,

Yadda take hura masa iskar slow ba ƙaramin ratsasa yakeyi ba da shiga jikinsa,

Sosai yayi dauriyar ganin bai jawota jikinsa ba,

Wani ni'imtaccen bacci ne ya kwashesa wanda baisan lokacin da ta sulale ta gudu ba,

Sai da aka fara kiraye kirayen sallar magrib kafin yayi firgigit ya tashi,

Ganin bata nan yasa yayi hanyar banɗaki,

Bai wani jima ba ya fito ɗaure da towel kafin a gaggauce ya shirya jikinsa ya nufi masallaci,

Ana idarwa ya nufi part ɗin hajiya dan shi kansa ya gaji da zaman ɗakinnasa,

A part ɗin ya tarar da da yawan yaran gifan musamman maza inda kowwa yayi masa sannu kafin aka shiga hirarraki,

suna haka su baba ummaru da yan uwansa suka shigo inda yaran suka sassakko dan basu gurin zama,

To shima dai zayyad miƙewa yayi saida suka zazzauna kafin ya zauna ya gaishesu suka yimasa ya jiki,

daga haka aka cigaba da hira har lokacin sallar issha,

bayam sun dawo daga sallar issha nan ma part ɗin hajiya suka dawo amma har yanzu shiru baba isuhu bai dawo ba,

hakan yasa baba ummaru ya lira ya tambayeshi ko lafiya?

bayan sun gaisa yake basu uzurin dubo abokin kasuwancinsu da gamayyar ƙungiyar kasuwa ta wakilta su amma yanzu zai dawo,

Da haka baba ummaru ya kashe wayarsa kafin suka cigaba da hira,

_____tun bayan issha suka gama shirin su kaf tareda saka farin gam ajikin emblope ɗin kafin suka hawo motar merru suka kama hanyar gidansu zayyad,

ba ƙaramin nishaɗi da farinciki merry takejiba yayinda ga baki ɗaya fareeda ta rasa abinda yakeyimata daɗi ,

Gaban tane ke wani mugiwar faɗuwa gani take batayiwa zayyad halacci ba datazama mai tona asirinsa amma wata zucoyar nacemata in batayi hakan ba zayyad zai kuɓuce mata na har abada,

Sai wajejen ƙarfe tara suka ƙaraso ƙofar gidan kasancewar sun taradda ho slow akan hanya,

Sim ɗan jima a ƙofar gidan amma shiru babu yaro,

Suna nan wata mota tayo gidan wanda hakan ya tabbatar musu ɗayane daga a halin gidan,

but amma ta ya zasu bashi saƙon babu yaron aiki,

har ya ƙaraso basu gama yanke hukunci ba,

sai da ya kashe motarsa kafin ya buɗe gate ɗin yashiga da motar,

bai jima da shiga ba suka sami almajiri suka bashi emblope ɗin tareda bashi naira hamsin sukace duk wanda yasamu ya bashi yace abawa baban zayyad,

Sai da suka tabbatar yaron yashiga gidan kafin suka ja motar suka bar layin,koda yaron ya shiga gidan baiga kowa ba hakan yasakashi yin ɗan dabur dabur alamar neman wanda zai bawa,

daga can wajen parking space ya hango ana rufe mota hakan yasakashi nufar hanyar parcking space ɗin,

da sauri ya fara nufar wanda yagani dan ya nufi hanyar shiga gidan,

Ganin yana neman shigewa yasaka yaron ɗan ɗaga murya yace,

"wai gashi abawa baban zayyad inji wasu yʻan mata a waje"

Karaf maganar ta sauka akan kunnen mama babba wadda take a laɓe tana waya da aminiyarta hajiya ruƙayya,

Da mamaki tasake nanata maganar yaron,

"inji wasu yʻan mata kuma abawa baban zayyad?"

Cikin sauri ta fito daga malaɓarta tareda yo inda yaron yake dan karɓar saƙon,

Sai dai kuma ko kafin tazo ma tuni baba isuhu ya rigata tana ƙarasowwa yana miƙa hannu ya karɓi emblope ɗin tareda kallon yaron,

"yʻammata kuma"

Cikin rashin wayau irinna yara yace,

"eh acikin mota ma suke suka kirani sukabani"

Baba isuhu ya dafa kan yaron tareda sake cemasa,

"to kuma baban zayyad suka cemaka kodai ka manta zayyad sukace?"

"A'a wllhy baban zayyad sukace nabawa"

"Shi kenan jeka abinka ba damuwa angode kaji"

Ba tareda wata damuwa ba yaron ya kama gabansa kafin shima ya juya da nufin shiga gida,

Gamin mutum a tsaye yaso yaɗan razana shi saboda bai ga kowwa ba a farko,

Auziya yayi kafin yace,

"waye"

A daburce mama ta fara kame kame,

"uhm ummm dama uyyymmm dama naɗan fitone"

Daƙyar tasamu ta haɗa kalmar kafin tayi saurin yin gaba,

Sosai mamaki ya kashe baba isuhu ya tsaye shin me hakan yake nufi kenan,

Ganin ba amsa yasakashi yin gaba tareda mamakin wannan emblope ɗin kuma ace wai inji wasu yammata abawa baban zayyad shin kodai yaron yayi kuskurene?

To amma in zayyad suke nufin a bawa ai yasan bazasu rasa contact da zayyad ɗin ba dan haka koma meye zasu iya yinshi a waya ko yasamesu,

Any way dai bazai taɓa bawa kowa emblope ɗin ba batareda ya duba yaga abinda yake ciki ba,

koda ya shiga gidan direct part ɗin hajjaju ya wuce wanda hakan shine tamkar al'adar mutanen gidan,

Bayan yan gaishe gaiahe tsakaninsa da yan uwansa akan ɗan taɓa hira kafin kowwa ya fara tashi dan zuwa ga iyalansu,

Kamar kowa shima baba isuhu haka ya miƙe ya nufi ɓangarensa da nufin inya gama ganin abinda ke cikin emblope ɗin da safe ya bawa yayannansa,

To kasancewarsa ajazi dakuma kasancewar mutim mai iyali yasa yana shiga part ɗin bayan yɑn abubuwan al'ada da yagabatar kamar yadda yasaba sai kuma yashiga wata sabgar shaf ya manta da maganar emblope ɗin kwata kwata,

Kasancewar kayan daya ke jikinsa dama yasakasu wannan maimaicine yasa yana cirewa ammi ta sakasu acikin doesving ɗin ɗakinsa na wanki,

daga haka kuma aka mance da wani babi na emblope,

Washe gari tun da safe mama babba tashirya da nufin zuwa asibiti dubo wata daga danginsu,

Tana fita ta kirawo wayar hajiya ruƙayya ta faɗa mata inda zasu haɗu dan zuwa gurin boka,

A ɓangaren zayyad kuwa yau ba laifi yaɗan tashi da sauƙi hakan yasa yana dawowa daga masallaci yayi wanka kafin yasake kwanciya,

ƙarfe tara ammi da abba suka ahigo part ɗin dan duba jikin zayyad saidai ganin yana bacci yasa suka juya da nufin komawa,

Jin motsin mutum yasa zayyad shima ya farka tareda yin miƙa gami da salati,

Ganin ya farka yasa suka dawo,

tashi yayi zaune cikin girmamawa ya fara gaishesu,

Suma dai kamar koqane lokaci cikin nuna tsantsar so da kulawa suka amsa da yimasa ya jiki,

Sai a lokacin aaƙon kiya ya faɗowa baba isuhu a rai,cikin hikima ya fara tambayar zayyad ɗin shin ko akwai wani saƙo dasukayi da wani za'a kawo gidan?,

Cikin alamun rashin damuwa zayyad ɗin ya amsa masa da a'a,

Jin hakannema ya ƙara ƙarfafawa baba osuhu gwiwa akan lallai ya duba saƙon gudun kuskure,

Ganin yana niyyar makara yasa sukayiwa zayyad ɗin sallama ammi na sanar ɓasa cewa brek first ɗinsa na part ɗinta,

Shima zayyad ɗin ya amsa mata da cewar idan ya kimtsa zai shigo ya karya,

Suna fitowwa baba isuhu ya nufi gurin motarsa da nufin idan ya dawo zai duba saƙon ganin yanzu ya makara,

So bayan kowwa ya fita masu lactures ɗim safe ma sunfita saɓanin su khadija da zasu shiga ƙarfe ɗaya da rabi,

ita dai aminatu ganin mama ta fita yasa itama yau kwata kwata bata fito ba ta ƙule a ɗaki tana tunamin da bazai amfana mata komai ba,

Kamar kullum yau ma khadija ta gamawa hajjaju aikace aikacenta kafin ta shirya tsaf cikin riga da sket na atamfa tareda murza ɗauri mai matuƙar kyau,

Duk da bawata kwalliya tayiba face hoda data shafa amma dai kunsan shi mai kyau kome yayi kyau yake,

A hankali take tafiya cikin talunta mai ɗaukar hankali ta nufi part ɗin ammi,

A falo ta iske ammin dan itama tuni suka gama dukkan aikace aikacen su itada ummy kafin ummyn ta wuce gurin aminiyarta fateema,

Da sallama tashigo falon ammi ta amsa,ta duƙa ta gaisheda ammin kafin tasamu guri a kusa da ammin ta zauna,

Sun ɗan fara taɓa hira cikin dabara ammi ke sako mata magamar yaya zayyad da irin karamcinsa da ɗaukar ammin dayayi a matsayin uwa,

cikin salon manyance da dabara take muna khafdijar ba wai zayyad ya tsaneta bane a'a sai dai wasu halaye nata da bayaso dasuke sakawa tana ganin kamar tsana ce,

Suna cikin wannan maganar zayyad ɗin yashigo cikin shigar ƙananun kaya datayi matuƙar karɓarsa,

da sallama yashigo suka amsa itada ammin yasami kujera ya zauna ammi na tambayarsa ƙarfon jiki,

Cikin dabara ta ɗaga idanunta ta ɗan saci kallonsa dan tun a shigowwarsa shigarsa ta ɗan birgeta,

A rashin sa'a kuwa shima ita yake kallo hakan yasa taji wata muguwar kunya ta lulluɓeta,

Sai da ta ɗan murguɗa masa baki kafin ta ɗauke idanunta daga kansa,

Sosai murmushi ya kusa ƙwace masa kafin yayi nasarar danneshi ya wani haɗe rai,

Ɗan mintsininta ammi tayi kafin tayo firgigit tace,

"yaya zayyad ina kwana,ya jiki"

Ta faɗa tareda turo baki wanda ammi bata ganiba amma shi sarai akan idanunsa,

"haɗomin breack ki kawomin"

Shine kawai abinda yace mata,

"ɗan iko mugu kawai"

Ta faɗa a ƙasan maƙoshi wanda babu wanda yaji acikinsu,

Kamar bazata tashi ba amma dai ta daure saboda idanin ammi taje ta haɗo masa ta kawomasa,

Yakusa minti biyar kafin ya miƙe yafara ci,

Bai wani ci sosai ba ya koma kan kujerar yasake kwanciya,

Ganin ya gama yasakata tashi ta ɗauke kayan tun kafin ammi tayi ƙorafi,

Ko kafin ta dawo ma ammin ta tashi a hanya suka haɗu dan haka tace mata ta je ɗakin abbansu ta ɗakko manyan kayan cikin basket ɗinsa ta kawo gali zai zo yanzu ya karɓa,

Ammi na gama faɗa ta wuce ɗaki dan gabatar da nata uzurin kafin khafija ma tawuce ɗakin abba,

Tana zuwa ta kwaso kayan ta taho,

Lokacinda tazo falo ya sauko ƙasa yawani baje ƙafafu,

Ai kuwa tsautsayi tana gittawa yasa mata ƙafa ta faɗa kan kujera kayan kuma suka zube,

Zubewar da kayan sukayine yasaka emblope ɗin tarwatsewa aikuwa hotunan suka bayyana a ƙasa a watse,

Ba ƙaramin tashin hankaline ya ziyarcesu gabaki ɗayansu ba ganin wannan mugun bala'in a ƙasa kuma daga cikin kayan abban,

"INNALILLAHI WA'INNA ILAIHIRRAJI'UN,shine kawai kalmar da suke maimaitawa gabaki ɗayansu,

tuni zayyad ya jiƙe da wani uban gumi wanda zaka iya rantsuwa ruwa aka kwara masa,

Saɓanin khadija da hawaye suka ɓallewa fuskarta kamar famfo,

jin motsin ana shigowwa shi ya ƙara tada hankalinsu gabaki ɗaya musamman ma dasuka fara jiyo mitar hajjaju,

Har ta zuro ƙafarta cikin falo gabaki ɗaya zayyad ya gama sarewa dacewar yau ranar tonon asirinsa ce wadda bazai taɓa fatan ko maƙiyinsa ya kasance aciki ba,

Wata uwar sifa khadija tayi ta baza babbar rigar abban gabaki ɗaya a ƙasa tareda malalewa akanta ta rife hotunan,

Har lokacin kuma hawayen basu daina ambaliya a idanunta ba,